# KATARI WAJEN FAHIMTAR TAUHIDI


**WALLAFAR**

ABDULLAHI BN SULAIMAN AL-MUHANNA

*[Cikin Harshen Hausa]*

**FASSARA**

SIRAJ BALA UMAR

**WANDA YAYI BITA**

JUNAID ISA IBRAHIM



Bugu na Farko

1441/2020

# التسديد لفهم التوحيد

إعداد:

عبد الله بن سليمان المهنا

ترجمة: سراج بلا عمر

مراجعة: جنيد عيسى إبراهيم

# KATARI WAJEN FAHIMTAR TAUHIDI


**WALLAFAR**

**ABDULLAHI BN SULAIMAN AL-MUHANNA**

***[Cikin Harshen Hausa]***

**FASSARAR**

SIRAJ BALA UMAR

**WANDA YAYI BITA**

JUNAID ISA IBRAHIM



*Bugu na Farko*

*1441/2020*

بسم الله الرحمن الرحيم

**DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JINƘAI**

**GABATARWA**

Dukkan yabo ya tabbata ga Allah, tsaira da aminci su tabbata ga manzon Allah, da iyalansa da sahabbansa, da wanda ya ƙaunace shi.. bayan haka:

Waɗannan darussan Tauhidi ne a taƙaice, na rubuta su ga masu bibiyata a tashar (NAHRUL JUMAN), tasha ce ta koyar da Tauhidi a kafar WhatsApp.. wani cikin ‘yan uwa masu daraja ya ba ni shawara a bugasu a wani kundi domin ya fi wanzuwa da sauƙin samuwa, sai na amsa masa, ina mai rokon Allah - Maɗaukaki - Ya sanya wannan aiki ya zama tsantsa domin zatinSa mai girma, Allah Shi ne abun dogaro.

Abdullahi bn Sulaiman al-Muhanna

Birnin Riyadh

14/4/1414

## (1)

### (SHIMFIƊA)

Ina son farawa a wannan sabon karatu mai dogon zango mai suna **(KATARI WAJEN FAHIMTAR TAUHIDI).**

- A ciki zan yi bayani -in sha Allah- game da wasu al-amura da suke warware Tauhidi, ko suke warware kamalarsa ta wajibi.

*Hakika kishiyar abu ita ke bayyana kyawunsa*

*ai da ma da kishiyoyi ne abubuwa suke bayyana.*

- Wanda ya san barna zai samu damar kiyayarta. Allah - Maɗaukaki - Ya ce: ***{Irin haka ne muke bayanin ayoyi, domin hanyar masu laifi ta fito fili}***[1].
- A cikin wannan gabatarwa zan yi bayanin ma'anar maganar malamai [cewa]: Wannan aikin yana warware Tauhidi. Da maganarsu [cewa}: Yana warware kamalar Tauhidi ta wajibi..
- Fadinsu cewa yana warware Tauhidi, ai wanda ya aikata shi babu wani abu na Taihidi da ya rage masa, ya fita kenan daga tauhidi zuwa shirka ko kafirci,

***Misalinsa:*** Shi ne rokon wanin Allah, shirka ce wadda take warware Tauhidi.

- Fadinsu cewa yana warware kamalarsa ta wajibi, ai yana fadawa cikin shirka karama, aiki ne haramtacce, sai dai ba ya fitar da mai aikata shi daga Tauhidi, zai zama akwai Tauhidi a tare da shi sai dai tauyayye ne a sakamakon aikinsa da ya aikata ko maganarsa, misalinsa: Yin rantsuwa da wanin Allah, haramun ne kuma shirka ce karama, sai dai ba ta fitarwa daga Tauhidi.
- Ya riga ya gabata a shirimmu mai dogon zango (saukaka asalai na Akida) bayanin ma'anar Tauhidi da nau'o'insa da ma'anar (LA'ILAHA ILLAL LAAH).

---

1 - Surat al-An'am: Aya ta 55.

- A can ne muka yi bayanin abin da ya ke jawo karkacewar wadanda suka karkace daga cikin Banu-Adam [mutane] daga Tauhidi zuwa shirka..
- Mun yi bayanin wani abu na nau'o'in zakewa a kan salihai, wanda yana daga cikin manyan dalilai na karkacewa.. sabo da haka babu bukatar maimaitawa, wanda hakan ta tsere masa sai ya duba shi a tashata ta (telegram) yana can an adana shi.
- Ina son jan hankali cewa wanda wani abu ya rikice mas, ko ya ke son tattaunawa, babu laifi ya turo min sako kai-tsaye ta lambar da aka sanya a kasan wannan littafi.

Muna rokon Allah Ya kula da mu bakidaya da rahamarSa, Ya shiyar da mu zuwa ga magana da aiki mai kyau, lallai Shi Mai ji ne, Mai amsawa ne,

*Tsira da amincin Allah su tabbata ga annabi Muhammad da iyalansa da sahabbansa bakidaya.*

****

**(2)**

## [SANAYA KAMBU DA GURU DA AWARWARO DOMIN MAGANCE RASHIN LAFIYA KO MAGANIN KAMBUN BAKA SHIRKA NE)

- Wasu mutane suna sanya guru a hannayensu ko su rataya a wuyansu.
- Ko su sanya abin da ake cewa (shudin ido) a cikin motocinsu, domin maganin kambun baka – bisa rayawarsu-
- Wasu ma takalmi su ke rataya wa.
- Wasu kuma suna sanya hoton kunamu ko kunkuraye da sauran abubuwa.. suna tsammanin za su tsare su daga shaidanu, ko su yi musu maganin kambun baka, da makamancin haka.
- Wasu matasa suna sanya awarwaraye, suna masu raya cewa za su ba su kuzari, da karsashi.
- Duk wannan yana daga cikin raunin imani da Allah, da raunin dogaro gareshi… aiki ne na haramun, kuma shirka da Allah ne, muna addu'a Allah Ya ba mu lafiya.
- Shin yanzu wanda ya ke da hankali ko yaya zai yi zaton wadannan shirmen abubuwa za su kareshi daga kambun baka da shafar aljanu da sauransu, ko kuma su ba shi wani kuzari?

Sai dai wasu zaunannun abubuwa ne na Jahiliyya da mutane suke rawaito wa juna, wanda wajibi ne a kawar da su.

- Allah SWT Ya ce: ***[Ka ce: Ku ba ni labarin abubuwan da ku ke roko ba Allah ba; idan Allah Ya yi nufin cutarwa a gareni shin za su iya yaye min cutarSa?)*** [1] Al-ayah.
- Wadanda suke rataya wadannan abubuwa, a hakika suna neman suyi musu abin da ba su da mallakarsa kuma ba za su iya halittatrsa ba, sun bar wanda ya mallaki amfanarwa da cutarwa, Shi ne Allah – SWT -.
- An karbo daga Imran dan Hussain - Allah Ya kara yarda da shi - **"Lallai annabi - Sallal laahu alaihi wa sallam - ya ga wani mutum ya rataya wani zobe na tagulla, sai ya ce da shi: "Mene ne wannan?" sai ya ce: Maganin rauni [gazawa] ne, sai ya ce: "Ka cire shi, domin ba zai kara maka komai ba sai raunin [gazawar], hakika da za ka mutu da shi a jikinka, ba za ka rabauta ba har abada"**[2].
- Wannan mutumin ya rataya zoben tagulla a hannunsa, wani ma'adani ne, yana so ne wannan zoben ya yaye masa wata cuta da ake kira da *wahina* [rauni ko gazawa], Sai Annabi - Sallalhu alaihi wa sallam - ya hanashi ya yi masa gargadin cewa ba zai taba samun rabauta ba, da zai mutu yana jikinsa ba zai rabauta ba, sai hakan ya nuna haramcin wannan aikin.

### 🕮 SHINJ RATAYA WADANNAN ABUBUWAN SHIRKA NE?

- Eh, idan ya kudirce cewa suna da mallakar amfanarwa ko kore cutarwa koma bayan Allah, wannan shirka ce mafi girma, mai fitarwa daga addinin Musulunci…
- Idan bai kudirce haka ba, sai dai ya yi zaton su din dalili ne wajen amfani da kawar da cuta, to, karamar shirka ce, shirka karama kuma ta fi manyan zunubai girma.

***Darasi na biyu ya kare da godiyar Allah.***

****

1 - Surat al-Zumar: Aya ta 38.
2 - Ahmad ne ya rawaito shi.

## (3)
## [RATAYA LAYU DA TSARI)

- **LAYOYI NAU'I BIYU NE:**

1) **Daga Al-kur'ani**
2) **Daga wanin Al-kur'ani**

- Annabi - SAW - ya ce: **"Lallai tawaida da layu da maganin mallaka shirka ne".**[1]
- Wasu abubuwa ne da da wasu masu tawaida ko matsafa suke raya cewa suna maganin kambun baka…
- Idan abin da aka rataya an rubuta sakandamai na shirka da neman tsarin shaidanu, to, babu kokonto cewa haramun ne, kuma sanya su shirka ne, muna rokon Allah samun lafiya.
- Idan abin da aka rataya Al-Kur'ani ne a ciki kawai, to, haramun ne shi ma, saboda gamewar hadisin da ya gabata, kuma saboda rataya su dalili ne da zai jawo wulakanta su domin za su iya faduwa a kasa daga [jikin] yaron, kuma da sunan Allah ko kuma ya shiga bayan gida da su, alhali da zancen Allah - SWT - a ciki.
- Abin da ya fi wannan girma kuma shi ne ratayuwar yaro da su alhalin shi a yawanci bai san abin da yake ciki ba, sai ya kudirce cewar kariyar [tsarin] a dalilin wadannan fatu da tsumma ne.
- Daga Abdullahi dan Ukaim mar'fu'i: **"Wanda ya rataya wani abu za a bar shi da shi"**[2].
- Ma'anar Hadisin shi ne cewa wanda ya ratayu da wani abu daga cikin wadannan abubuwa Allah Zai bar shi, kuma ya jingina shi zuwa abin da ya ratayu da shi.
- A [Hadisi] ingantacce daga Abu Bashir al-Ansariy - Allah Ya kara yarda da shi - cewa ya kasance tare da manzon Allah - Sallal lahu alaihi wa sallam - a cikin wata daga tafiyoyinsa, sai ya tura dan aike: **"kada a bar wani abin wuya a wuyan rakumi ko tsarkiya ko wani rataye face an tsinke shi".**

1 -Ahmad da Abu-Dawud ne suka rawaito shi.
2 -Ahmad da Tirmizi ne suka rawaito shi.

- Sai ya nuna cewa ba ya halatta a rataya wa dabbobi abin wuya sabo da maganin kambum baka da makamancinsa, kuma wajibi ne a tsinke shi, a ratayu [dogara] da Allah – SWT-.

## 🕮 TO, MENE NE MADADIN WADANNAN LAYU?

- Madadin shi ne neman tsari ta hanyar Azkaar na shari'a, daga ciki a kwai Ayatul-Kursiyyi, da kula-uzai da sauran Azkaar da tsari na Shari'a.
- Game da wannan sai a duba littafin Azkaar na al-Nawawiy - Allah Ya ji kansa -.
- Da littafin al-Wabil Al-sayyib na Ibnul-Kayyim - Allah Ya ji kansa -.
- Da littafin Tuhfatul Akhyaar na Sheikh Ibn Baz - Allah Ya ji kansa -.
- Da littafin Hisnul Muslim na Sheikh Sa'id bn Wahaf al-Kahtaniy - Allah Ya ji kansa -.
- Ka bar littafin nan na [Dala'ilul Khairaat] Na Malam al-Jazuliy, sabo da a cikin sa akwai sabawa [shari'a] da bidi'o'i.

Allah ne Masani, tsira da amincin Allah su tabbata ga Annabimmu Muhammad.

***Darasi na uku ya kare da godiya ga Allah.***

****

## (4)

## [TABARRUKI]

- TABARRUKI shi ne neman albarka.
- Albarka: Ma'anarta ita ce: Lazimtar alheri da tabbatarsa, habakarsa a cikin abu.
- Albarka daga Allah take, yana sanyata a wasu abubuwan halittaraSa.

### 🕮 SABODA HAKA NE [YA ZO] A CIKIN AL-KUR'ANI:

- ***[Albarkatun Allah sun yawaita, [Shi ne] mafi kyawun masu halitta)*** [1]
- ***[Albarkatun sunan Ubangijinka sun yawaita)*** [2].
- ***[Albarkatun sunan Ubangijinka sun yawaita wanda Ya saukar da Al-Furka)*** [3]
- ***[ Albarkatun sunan Ubangijinka sun yawaita wanda Ya a hannunSa mulki ya k)*** [4]
- Saboda wannan ake neman albarka daga Allah.
- Hakika Allah Ya sanya albarka a cikin wasu daga abubuwan halittarSa kamar ruwan Zam-zam, ya sanya zancenSa ya zamo mai albarka, kamar yadda Ya ce: [ Littafi ne da muka saukar da shi mai albarka)[5], ya sanya Dakin [Masallacin] Harami ya zama waje mai albarka… Da sauransu.

### NEMAN TABARRUKI AKWAI NA SHARI'A DA WANDA AKA HANA.

- Yana daga cikin na Shari'a Tabarruki da zatin Annabi - Sallalhu Alaihi wa sallam - a rayuwarsa, hakika sahabbabi sun kasance -Allah Ya yarda da su- suna neman tabarruki da ruwan alwalarsa - Sallalhu Alaihi wa sallam - , da kuma guminsa da makamancin haka na irin abubuwan da suka baro jikinsa - Sallalhu Alaihi wa sallam.. Kuma ya kasance yana tabbatar da su a kan haka - Sallalhu Alaihi Wa sallam -.
- Amma a yanzu babu abin da ya inganta na wani abu na manzon Allah - Sallalhu Alaihi Wa sallam - da za a yi tabarruki da shi kwata-kwata.

---

1 -Surat al-Mu'minun. Aya:14.
2 -Surat al-Rahman: Aya 78
3 -Surat al-Furkan: aya 1
4 - Surat al- Mulk: Aya: 1
5 - Surat Saad: Aya ta: 29.

- **SHIN ZA A YI TABARRUKI DA AHLUL BAITI DA SALIHAI KIYASI DA ANNABI** - Sallalhu Alaihi Wa sallam-?

- Ba ya halatta a nemi tabarruki da kowa idan ba annabi ba - Sallalhu Alaihi Wa sallam -, kuma ba a kiyasin wani a kansa, sahabbai ba su nemi tabarruki da Abubakar ba ko Umar ko Ahlul baitin Annabi - Sallalhu Alaihi Wa sallam -.
- Daga cikin mafi girman abin da ake neman tabarruki da shi Al-Kur'ani ne zancen Allah - Madaukakin Sarki- , Allah - SWT - Ya ce: ***﴿Littafi ne da Muka saukar da shi mai albarka﴾***[1]. Manzon Allah - Sallalhu Alaihi Wa sallam - ya fada game da Surat al-Bakara: "Riko da ita albarka ne"… Karatun Al-Kur'ani yana jawo albarka a cikin gida , da arziki da dukiya da kuma lokaci.
- Daga cikin neman tabarruki da Shari'a ta yarda da shi akwai shan ruwan zam-zam domin samun albarka, annabi - Sallalhu Alaihi Wa sallam - ya ce: Hakika ta na da albarka"

## DAGA CIKIN NEMAN ALBARKA DA AKA HANA:

- Neman tabarruki da duwatsu da bishiyoyi kamar aikin 'yan Jahiliyya, Allah - SWT - Ya ce: ***﴿Ku ba ni labarin Lata da Uzza, da Manata da ta ukun su da ban﴾***[2]. [Har karshen] ayoyin. Sun kasance suna neman tabarrukin a wajensu na fatan amfani ko gusar da cuta.
- Daga ciki akwai neman tabarruki da kaburburan annabawa da salihai, da abin da ake kira da *Atabat* masu tsarki, da sumbantar tagogin kaburbura, da wuraren zama da yin sallar salihai, irin abin da ake kira da makamaat, haka nan neman tabarruki da da kasar kabari, ko abin da ake kira da turbayar Karbala, daga ciki akwai neman tabarruki da iskar kabarin wane daga cikin salihai, daga ciki akwai abin da ake kira da neman madadi daga rayukan salihai, Da neman tabarruki da yawun salihai kamar yadda sufaye suke aikatawa tare da shehunansu, duk wannan yana daga cikin neman tabarrukin da aka hana , kuma haramun ne, daga cikinsa ma akwai wanda shirka ne.

---

1 - Surat Saad: Aya ta: 29.
2 - Surat al-Najm: Aya: 19 – 20.

- Daga Abu Wakid al-Laithiy - Allah Ya yarda da shi - ya ce: “Mun fita tare da manzon Allah - SAW - zuwa Hunain alhalin muna sababbun fita daga kafurci, Mushirikai suna da wata bishiyar magarya da suke dukufa a wajenta, suna rataye makamansu a jiki, ana cewa da ita ma’abociyar rataye, sai muka wuce ta wajen wata magarya, sai muka ce ya ma’aikin Allah, ka sanya mana ma’abociyar rataye kamar yadda suke da ma’abociyar rataye, sai manzon Allah - SAW -ya ce: Allahu Akbar! Lallai haka tsarin ya ke, kun fada kamar yadda Banu Isra’il suka ce da Annabi Musa: ***[Ka sanya mana abubuwan bauta kamar yadda suke da abubuwan bauta, sai ya ce: Lallai ku mutane ne masu wauta ]***[1], lallai za ku hau tsarin wadanda suka kasance kafinku”[2].
- Sai Annabi - SAW - ya dauki neman tabarrukin da suka yi da magarya a matsayin daukarta a matsayin abar bauta,, domin abin bauta shi ne wanda ake nufi da neman amfani ko kawar da cuta, kuma babu wanda ya ke da mallakin haka sai Allah – SWT -.

***Darasi na hudu ya kare da godiyar Allah.***

****

1 - surat al-A’raaf: Aya 138
2 - Tirmizii ne ya rawaito shi, kuma ya inganta shi.

**(5)**

## (YANA DAGA CIKIN SHIRKA DA ALLAH YIN YANKA GA WANIN ALLAH)

- Yanka yana daga cikin ibadu da Allah - SWT - Ya ke so.
- Allah - SWT - Ya ce: ***(Ka yi Sallah domin Ubangijinka, ka soke [abin layyarka)***[1].
- Abin nufi da yanka shine mai yankan ya yi kyautar abin da ya mallaka ga Allah SWT, sai ya zubar da wannan jini yana mai neman kusanci zuwa ga Allah – SWT -.
- Allah - SWT - Ya ce: ***[Namansu ko jininsu ba zai samu Allah ba, sai dai Takawarku ita ce za ta zameShi]***[2].
- Allah - SWT - Mawadaci ne daga yankammu, mu ne masu bukata ga samun ladan Allah – SWT -.
- Neman kusanci ga Allah - SWT - ta hanyar yanka yana kasancewa ne ta hadaya da layya da ragon suna da bakance.
- Sabo da sanin Annabi - SAW - ga falalar yanka sai ya yi hadaya da rakumi dari a hajjinsa, da hannunsa ya soke sittin da uku daga ciki.
- Idan ya kasance yanka yana da wannan matsayi da falala, to, hakika sarrafata ga wanin Allah shirka ne, kamar Sallah da Addu'a ga wanin Allah daidai wa daida.
- Saboda haka Allah - SWT - Ya ce: ***(Ka ce: Lallai Sallata da Nusuk dina***) ai: yankana - ***[da rayuwata da mutuwata [duk]na Allah ne Ubangijin talikai. Ba shi da abokin tarayya)***[3].
- Kamar yadda ba shi da abokin tarayya ga Allah a sallah =, to, haka ma ba shi da abokin tarayya a yanka.
- [Annabi] SAW ya ce: **"Allah Ya la'anci wanda ya yi yanka ba don Allah ba",** duk wanda ya yi yanka don wanin Allah, to, ya kai kansa ga la'antar Allah, Allah Ya tsare mu.

1 - Surat a--Kauthar: Aya 2.
2 - Surat al--Hajj: Aya ta 37
3 -Surat al--An'am: Aya ta 163

## 🕮 YANA DAGA SALO-SALO NA YIN YANKA DOMIN ALLAH:

1) Yin yanka domin waliyyai a maulidansu – ko da kuwa an ambaci sunan Allah a kai- domin nufin zuciyar shi ne fuskantar matattu,, da wannan sai ya zama yanka ne ba don Allah ba, ambaton Allah ba ya sanya su su zama halal.
2) Abin da ya fi hakan shi ne idan aka ambaci sunan wanin Allah a kai, kamar a lokacin yankan a ce: Da sunan *kuros* ko da sunan Masihu.

Allah - SWT - Ya ce: ***(kadai Allah Ya haramta muku mushe da jini da naman alade da abin da aka kururuta wanin allah a kai)***[1] .

3) Daga cikin salo-salo na yanka ba don Allah ba, akwai bakance domin Ahlul baiti, kamar bakancen 'Yan Shi'a ga Al-Abbas da Hussain da sauransu daga cikin Ahlul Baiti, duk wani bakance ga wanin Allah, to, haramun ne kuma shirka ne, idan ya kasance yanka ne, to, shi ne mafi tsananin laifi.
4) Yana daga cikin salo-salo na yanka ba don Allah ba akwai yin yanka saboda bullowar sarki..

   [Malam] al-Nawawi - Allah ya yi masa rahama - ya ce: Sheikh Ibrahim al-Marwazi daga cikin mutanemu ya ambata cewa abin da ake yankawa lokacin tarbar sarki domin neman kusanci, Mutanen Bukhara sun ba da fatawar haramcinsa; sabo da yana daga cikin abin da aka kururuta wanin Allah - SWT - a kansa.
5) Yana daga cikin salo-salo na yin yanka ba don Allah ba, yin yanka a kofar sabon gida, domin neman tsari daga aljanu ta hanyar haka.
6) Yana daga cikin salo-salo na yin yanka ba don Allah ba, yin yanka domin girmama wanda ya dawo daga dubiyar rashin lafiya da makamancinsa, ta hanyar yi masa yanka a lokacin wucewarsa da motarsa ko kuma a kofar gidansa, tare da sanin mai yankan cewa ba zai ci komai daga ciki ba, sai ya zama manufar wannan yankan ita ce

1 - Surat al--Nahl: Aya ta 115.

zubar da jinin ce – Allah Ya tsare mu- wannan kuma shi ne yankan da ba ya halatta a yi shi sai ga Allah, sabo da manufar yin yanka saboda Allah shine zubar da jinin dominSa – SWT -, domin Shi Mawadaci ne daga naman da jinin kamar yadda [bayani] ya gabata.

7) Yana daga cikin salo-salo na yin yanka ba don Allah ba, a kwai yin yanka domin aljanu bisa umarnin mai yi tsafi, ko boka domin warware sihiri, ko domin binciko wani abu da ya bata da makamancinsa, duka wannan yana daga cikin shirka da Allah, muna neman tsarin Allah daga hakan.
8) Yana daga cikin salo-salo na yin yanka da aka haramta akwai na bukukuwa na mushrikai na wurare, hana yin hakan toshe baraka ne ta rayar da bukukuwan mushrikai a wurare ko kuma yin kamaceceniya da su.

***Duk abin da aka yanka ga wanin Allah, to, cin sa haramun ne.***

***Darasi na biyar ya kare da godiya ga Allah.***

****

**(6)**

## (YANA DAGA CIKIN SHIRKA YIN BAKANCE GA WANIN ALLAH)

- Bakance shi ne mutum ya lazimtawa kansa wani aikin ibada da bai lazimce shi a shari'ance ba.
- Fararda shi [yin sa matakin farko] *makaruhi* ne; sabo da fadin Annabi – SAW -: **"Kada ku yi bakance, hakika bakance yana zuwa da alheri, kawai dai ana fitarwa ne [abin alheri] daga marowaci".**
- Wanda ya yi bakancen zai yi da'a ga Allah, to, ya yi masa da'a, wanda kuma ya yi bakancen zai saba masa, to, kada ya saba masa.
- Cika bakance ibada ce ga Allah, Allah - SWT - Ya ce: ***{suna cika bakance, kuma suna tsoron wata rana da sharrinta ya kasance mai yaduwa}***[1]
- Allah - SWT - Ya ce: ***{Abin da ku ka ciyar na ciyarwa ko ku ka yi bakancensa na wani bakance, to, Allah Yana sane da shi}***[2].
- Idan ya kasance ibada ce , to, sarrafata ga wanin Allah shirka ce.
- Bakance ga wanin Allah sabo ne bisa ittifakin [haduwar] malamai, ba ya halatta a cika shi.
- Da zai yi bakance sai ya ce: Idan Allah Ya warkar da mara lafiyata, to, ya zama lallai a kaina zan yanka akuya ga Shehu Abdul-Kadir, da nufin neman kusanci zuwa gareshi, da riko da shi a matsayin tsani, kuma mai ceto zuwa ga Allah , to, wannan bakance barna ne haramun ne, ba ya halatta a cika shi.
- Irinsa ne bakancen da ake yankawa ga [sayyidina] Hussain da Ahlul Baiti a Ashura, da abincin da ake yi a wannan rana, ko abin da ake kira da Arba'in [din Imam Hussain], suna kudirce cewa akwai waraka da albarka a cikinsa.. duk wannan bakance ne ga wanin Allah , ba ya halatta a cika shi.
- Irinsa ne bakancen da ake yi wa waliyyai, kamar a tafi zuwa kabarin waliyyi [mutum] ya ce: Ya sayyidiy in aka warkar da mara lafiyana ko da na ya ci jarrabawa zan ba ka *gold* irin kaza-da-kaza, duk wannan yana

---

1 - Surat Al--Insan: Aya ta 7.
2 - Surat al--Bakara: Aya ta 27.

daga cikin shirka, kuma a cikinsa akwai kamanceceniya da aikin Jahiliyya [da suke yi] a wajen bishiyoyi da duwatsu.

- Duk wannan –muna rokon Allah yafiya- bisa kudircewarsu cewa mamacin [da suke riko] ya san da bakancen da suka yi masa, ko kuma yana da tasarrufi a al'amura koma bayan Allah - SWT - ba -, wannan shirka ce a *Rububiyya* da *Ilahiyya*.
- Kudirce cewar yana da tasarrufi kuma yana da masaniya shirka ne a *Rububiyya*, yin bakance gareshi shirka ne a *Uluhiyya*.

Muna rokon Allah shiriya ga kowa.

***Darasi na shida ya kare da godiyar Allah.***

****

## (7)

## (NEMAN TSARI DA WANIN ALLAH)

### NEMAN TSARI:

- Shi ne fakewa da neman kariya da neman mafaka.

### HAKIKANINSA:

- Gujewa daga wani abu da kake tsoronsa zuwa wanda zai kareka daga shi.
- Mai neman tsarin Allah, hakika ya guje ne daga abin da zai cutar da shi ko ya halakar da shi zuwa Ubangijinsa Mamallakinsa.
- Wannan zai bayyana cewa neman tsarin Allah bauta ce a gareshi – SWT -.
- Allah - SWT - Ya ce: ***(Idan wani mai ingiza daga shaidan ya ingijeka, to, ka nemi tsarin Allah, lallai Shi Mai Ji ne, Masani ne)***[1].
- Allah - SWT - Ya ce: ***(Ka ce: Ina neman tsarin Ubangijin safiya)***[2].
- Idan ya zama Allah Shi ne Ubangijimmu Mamallakimmu abin bautarmu, to, ba mu da wajen fakewa [idan mun razana] a lokacin tsanance-tsanace idan ba Shi ba, ba mu da mafaka daga wajenSa sai dai zuwa gareShi.
- Saboda haka Allah Ya yi umarni a nemi tsari da mafaka zuwa ga Shi a lokacin tsanance-tsanace a al'amuran da ba mai iya wa sai Shi – SWT -.
- Allah - SWT - Ya ce: ***(Ka ce: Ya Ubangiji ina neman tsarinKa daga busar shaidanu, ina neman tsarinKa kada su halartoni)***[3].
- Yana daga cikin abin da mushrikai na farko suke a kai cewa sun kasance suna neman tsarin aljanu daga [sharrin] junansu, Allah - SWT - Ya ce: ***(Kuma lallai yadda lamarin yake wasu mazaje daga mutane suna neman tsarin wasu mazaje na aljanu, saboda haka suka kara musu girman kai).***
- [Malam] Mujahid ya ce: Sun kasance idan suka sauka a wani kwari suna cewa: Muna neman tsarin shugaban wannan kwari, sai suka kara musu girman kai.
- Ya ce: Sun kara wa kafirai dagawa.

---

1 - Surat Fussilat: Aya ta 36.
2 - Surat al--Falak 1.
3 - Surat al--Mu'minun: Aya ta 97 – 98.

- Annabi - SAW - ya shiryar da wanda ya sauka a wani masauki ya ce: **"Ina neman tsarin kalmomin Allah cikakku daga sharrin abin da ya halatta".**
- Lallai malamai sun yi *Ijma'i* a kan cewa ba ya halatta neman tsari da wanin Allah, kamar neman tsari da shaidanu da na cikin kabari.
- Idan neman tsarin ya kasance da Allah da kalmominSa ibada ne, kuma Tauhidi ga Allah – SWT -, to, hakika neman tsari da waninSa cikin abin da babu mai iya wa sai Allah, to, ya zama shirka da Allah.
- Kamar neman tsari da aljanu, da neman tsari da matattu daga [sharrin] makiya da suransu..
- Hakika sun kasance a zamanin Jahliyya idan ana neman mutum sai ya fake da kabarin wali wane, sai mai neman ya kame [ya hakura] daga neman cutar da shi, saboda ya shiga kariyar shehu, ya fake da shi, duk wanda ya nufe shi da wani mugun abu, to, ya kai kansa ga samun cutarwar waliyyin nan, gwargwadon mummunan kudirin da suke da shi, kuma gwargwadon abin da ya tsaya a zuciyarsu na kudiri game da matattu cewa suna amfanarwa ko suna cutarwa.
- Neman tsari da manzo SAW bayan rasuwarsa yana daga cikin wannan nau'in ..
- Sabo da wannan ne wasu daga cikin masu bege ga Manzon Allah suka karkace, kamar yadda al-Busiriy ya fada a kasidarsa:

*Ya mafi darajar halitta wa nake da shi da zan fake da shi*

*Idan ba kai ba a lokacin saukar abin nan mai faruwa mai gamewa*

Sai ya kore wa kansa samun wata mafaka idan abubuwan faruwa sun faru idan ba Annabi ba SAW, Haka [ya fada] da salo na iyakancewa da takaicewa, irin wannan kuwa ba na kowa ba ne sai Allah Shi kadai, Shi ne wanda bayi ba su da mafaka idan ba shi ba – SWT-.

- [Annabi] Muhammad - SAW - yana cewa game da kansa kamar yadda Allah Ya fada ***(Ka ce ba ni da mallakar wa kaina amfani ko cuta sai abin da Allah Ya so, da na kasance na san gaibu da na yawaita alheri,***

***da wani mummuna abu bai sameni ba, ni ban kasance ba sai mai gargadi ga mutanen da suke imani)***[1].

- Idan [annabi] SAW ya kasance bai mallakawa kansa amfani ko cutarwa a rayuwarsa ba, to, ta yaya zai mallakawa wani bayan rasuwarsa!!
- Kuma dai al-Busiriy ya ce:

*Idan bai kasance mai riko da hannuna ba a lokacin tashi [alkiyama]*

*A matsayin falala daga wajensa ba, to, ka ce kawai kafa ta gama zamewa*

A cikin wannan baiti da wanda ya gabaceshi akwai bijirewa Mahalicci – SWT -, da dogaro ga abin halitta cikin abubuwan da suke faruwa a a duniya da lahira.

Kuma wannan mawaki ya zo da rokon manzon Allah - SAW - da neman tsari da shi da sigar sharadi, kamar yadda Annabi Nuhu - AS - ya fada: ***(Idan ba ka gafarta min ba, idan ba ka yi min rahama ba, zan kasance cikin asararru)***[2].

Muna neman tsarin Allah daga shirka da rokon wanin Allah.

- [Ya zo] a cikin littafin Allah game da ranar Alkiyama [ranar da wani rai ba ya mallakawa wani wani abu, al'amarin na Allah ne a wannan ranar)[3].
- Wane abu ne [Annabi] Muhammad - SAW - ya mallaka ga wani!! Hakika al'amarin na Allah ne a wannan ranar.
- Abin nufi dai [shi ne] cewa neman tsarin Allah - SWT - tauhidi ne kuma Ikhlasi ne, neman tsarin waniSa cikin abin da babu mai ikon a kansa sai Allah, ko kuma neman tsarin aljanu da matattu da wadanda ba sa nan shirka ce mafi girma, Allah Ya tsare mu.

***Muna rokon Allah shiriya ga kowa ..***

***Darasi na bakwai ya kare da godiyar Allah.***

****

1 - Surat al-A'raaf: Aya ta 188.
2 - Surat Hud: Aya ta 47.
3 - Surat al-Infitar: Aya ta: 19.

**(8)**

## [ROKON WANI ALLAH YANA DAGA CIKIN SHIRKA]

- Addu'a tana daga cikin mafi girman ibadu, kai! Ita ce ma ibadar kamar yadda Annabi - SAW - ya ce: **"Addu'a ita ce ibada"**[1].

**ADDU'A NAU'I BIYU CE:**

- **ADDU'AR IBADA:**
- Ita ce bautar Allah da dukkan nau'o'in ibadu na sallah da yanka da bakance da azumi da hajji…
- Ko da babu wata siga ta tambaya da nema a ciki, mai ibada yana rokon Allah da aikinsa domin ya shigar da shi aljanna ya tseratar da shi daga wuta.
- **ADDU'AR ROKO:**
- Ita ce neman abin da zai amfani mai addu'a wajen samun amfani ko yaye cuta.
- Allah - SWT - Ya ce: ***[Ku roki Ubangijinku alhalin kuna kankan da kai da tsoro, lallai Shi ba Ya son masu ketare iyaka]***[2].
- Allah - SWT - Ya ce: ***[Kiran gaskiya ya tabbata gareShi]***[3].
- A cikin hadisi Kudusi Allah - SWT - Yana cewa: ***"Wa zai rokeni in amsa masa".***
- Ikhlasi wajen rokon Allah - SWT - yana wajaba kamar yadda Allah - SWT - Ya ce; ***(Ku roki Allah kuna masu tsarkake addini a gareShi)***[4] ai addu'a.
- Ikhlasi a cikin addu'a shi ne a roki Allah - SWT - Shi kadai, kada a yi tarayya da shi a cikin addu'a da kowa.
- Allah SWT Ya ce: ***[Kuma lallai masallatai na Allah ne, saboda haka kada ku bauta wa wani tare da Allah ]***[5].
- Allah - SWT - Ya ce: ***[Kada ka kira wanda ba zai amfaneka ba ko ya cutar da kai wanda ba Allah ba, idan ka aikata, to, ashe kana cikin azzalumai)***[6].

---

1 - Tirmiziy ne ya rawaito shi.
2 -Surat al-A'raaf: Aya ta 55.
3 - Surat al_ra'd: 14.
4 - Surat Gafir: Aya ta 14.
5 - Surat al-Jinn: Aya ta 18.
6 - Surat Yunus: Aya ta 106.

- Allah - SWT - Ya ce: ***(Wadanda kuwa ku ke bauta wa ba Shi ba su mallaki ko da rigar kwallon dabino ba. Idan kuna kiransu, ba sa jin kiranku, ko da ma sun ji, ba za su amsa muku ba; a ranar alkiyama kuma za su butulce wa shirkarku da su. Ba ko mai ba ka labari kamar Masani)***[1] sai Allah Ya kira rokonsu a matsayin shirka da su.
- Ayoyi game da hanin rokon wanin Allah ya wuce a kidaye su.
- Hakika 'Yan Jahiliyya sun kasance suna rokon annabawa da salihai suna neman cetonsu a wajen Allah, sai Allah Ya ba da labari cewa addu'arsu ba za ta amfanar da komai ba, sai ya ce: ***[Suna bauta wa abin da ba zai amfanesu kuma ba zai cutar da su ba koma bayan Allah, suna cewa wadannan sune masu cetommu a wajen Allah]***[2].

## ROKON WANIN ALLAH SHIRKA NE BISA IJMA'IN MUSULMAI

- Wanda ya ce: [a ba mu] madadi ya Manzon Allah.
- Ko [a ba mu] madadi ya Hussain.
- Ko [a ba mu] madadi ya Hassafiy.
- Ko ya ce: [a ba mu] madadi ya Aidaruus.
- Ko ya ce: Ku kula da yanayimmu a tare da ku ya Ahlul Baiti.
- Ko ya ce: Ka duba mu da idanunka ya Hussain.
- Ko ya ce: Ya Sheikh Abdul-Kadir ka agajeni, ko ka taimakeni, ko Ni dai ina cikin kulawarka.
- Duk wannan rokon wanin Allah ne, kuma shi ne Shirka mafi girma wadda ba a gafarta ta sai da tubar zara-bunu,,,
- Wanda ya mutu yana mai zarcewa a kanta shi ne wanda zai dauwama ya zama dawwamamme a cikin wuta, Allah - SWT - Ya ce: ***[Hakika yadda sha'anin ya ke wanda ya yi shirka da Allah , to, ya haramta masa aljanna , kuma makomarsa ita ce wuta)***[3].
- Allah - SWT - Ya ce: ***(Lallai Allah ba Ya gafarta a yi shirka da Shi)***[4], yana nufin ga wanda ya mutu yana mai zarcewa a kanta.
- Wanda ya ce wannan tawassuli ne da salihai … to, irin wannan bai fahimci shari'ar Allah ba, kuma bai fahimci komai a harshen Larabawa ba.

---

1 -Surat Fatir: Aya ta 13 – 14.
2 - Surat Yunus: Aya ta 18.
3 - Surat al-ma'ida: Aya ta 72.
4 - Surat al-Nisa': Aya ta 48.

- Tawassuli shi ne rikar tsanin da zai kusata ka zuwa ga Allah, wanda ya ke rokon wani ba Allah ba, to, kai-tsaye yana nema ne daga wanda ya ke roko abin da babu mai iko a kansa sai Allah, wannan kuwa ita ce shirkar.
- Hani daga wannan shirkar ya fi kowane aiki na gari karfi [muhimmanci], saboda da shi ne jahili ya ke tsira daga shirka da Allah – SWT -, ya ke kwatar kai daga igiyar bautarwar Dajjalai [bakaken makaryata] masu kitsa karya, wadanda suke bata masa addininsa, suke cin dukiyar mutane da barna.

***Muna rokon Allah shiriya ga kowa…***

***Darasi na takwas ya kare tare da godewa Allah.***

****

## (9)

## [CETO]

- Mushirikai a da sun makale a cikin shirkarsu da jelar {igiyoyin] ceto, kamar yadda [Allah] SWT Ya ce: ***(Kuma suna bautawa wanin Allah abin da ba ya cutar da su, kuma ba ya anfanar da su, suna cewa wadannan su ne masu cetommu a wajen Allah)***[1] .
- Sai dai Allah - SWT - ya yanke kwadayin mushirikai daga [samun] wannan ceton, ya bayar da labarin cewa shirka ne, Ya tsarkake kanSa daga shi, Ya kore [a samu] wani majibinci ko mai ceto ga halitta in ba Shi ba.
- Allah - SWT - ba Ya bukatar wanda zai taimakeshi wajen sadar da bukatu ga halitta, Shi [Allah] SWT Ya san dukkan bukatu duk da banbancin yare da murya.

**ALLAH SWT YA SANYA SHARADI BIYU NA KARBAR CETO WADANDA BABU TABBACINSU A NAN DUNIYA:**

1) **SAMUN IZININ YIN CETO GA MAI YIN CETON.**
2) **YARDA GA WANDA ZA ACETA**

- Allah SWT Ya ce: ***(Ranar da ceto ba zai amfani ba sai ga wanda ar-Rahman [Allah] Ya yi masa izini, Kuma Ya yarda ya yi magana)***[2].
- Saboda wannan hakika duk rokon Annabawa da waliyyai da salihai da hujjar samun cetonsu da albarkarsu daidai ya ke da aikin mushirikai na farko.
- Misalinsa a yanzu shi ne neman ceto daga Annabi – SAW- , shi ma yana daga cikin neman ceto wanda ba daidai ba, saboda sharadin ceton bai cika ba.
- Samun izinin daga Allah bai tabbata ba ga Annabi – SAW -, ta yadda ya riga ya bar duniya, kuma dangantakarsa da wahayi ta yanke.
- Na biyu lallai Allah ba zai yarda da aikin wanda za a ceta ba saboda ya roki wanin Allah.
- Lallai Allah ba Ya yarda da shirka.
- Allah - SWT - Ya ce: ***(Ba Ya yarjewa bayinSa yin kafurci***)[1].

---

1 - Surat Yunus: Ay ta 18.
2 - Surat Daha: Aya ta 109.

- Wanda ya roki Annabi - SAW - ko wani daga Ahlul baiti ko wani da waliyyai yana mai neman cetonsu, to, lallai wannan neman nasa yana daga irin jinsin abin da mushirikai na farko suke aikatawa, kuma shirka ne, neman ceto ne wanda ba daidai bakuma korarre.
- Lallai shaidan ya yi wasa da halittu [mutane] da yawa, yana nufin yanke dangantakarsu da Allah, ta yadda ya sanya musu jin cewa lallai sai sun riki masu ceto a matsayin tsani zuwa ga Allah, tare da cewa Allah Ya ce: ***(Ubangijinku Ya ce ku rokeni zan amsa muku )***[2] sai Ya yi umarnin a rokeShi batar da wani tsani ba.
- Wanda ya ke son ceton [Annabi] Muhammad – SAW-, to, sai ya nema a wajen Allah , ba a wajen [Annabi] SAW ba, saboda ceton mallakin Allah - SWT - nee ***[Ka ce ceto gabadaya na Allah ne]***[3].
- Sai ka ce: Ya Allah Ka azurta ni da ceton [Annabi] Muhammad – SAW-.
- Ko kuma: Ya Allah Ka bai wa Annabinka Muhammad cetona.

**WANNAN CETON ZAI KASANCE A RANAR ALKIYAMA, DAGA CIKIN DALILAN SAMUNTA AKWAI:**

- Yin ikhlasi a Tauhidi.
- Bibiyar mai kiran Sallah, sannan salati ga Annabi – SAW -, sannan fadin: **"Ya Allah Ubangijin wannan addu'a cikakkiya …."** Har zuwa karshen hadisin.

***Muna rokon Allah shiriya ga kowa..***
***Darasi na tara ya kare tare da godewa Allah.***

****

1 -Surat al-Zumar: Aya ta 7.
2 - Surat Gafir: Aya ta 60.
3 - Surat al-Zumar: Aya ta 44.

## (10)

## [ DAUKAR MAKABARTU A MATSAYI MASALLATAI)

- **ANNABI - SAW - YA HANA DAUKAR MAKABARTU A MATSAYIN MASALLATAI CIKIN DALILAI MASU YAWA.. DAGA CIKI AKWAI:**

- Hadisin [Nana] A'isha cewar Ummu Salamah ta fadawa manzon Allah - SAW - [labarin] wata coci da ta gani a Habasha da abin da ya ke cikinta na hotuna, sai ya ce: **"Wadannan su ne wadanda idan mutumin kirki ya rasu a cikinsu ko bawa na kirki sai su gina masallaci a kan kabarinsa, sai su yi wadannan hotuna a ciki, wadannan su ne lalatattun mutane a wajen Allah"**[1].
- Sai Annabi - SAW - ya yi bayanin cewa gina masallatai a kan kaburburan salihai yana daga cikin ayyukan Nasara, ba aikin Musulmai ba.
- Annabi - SAW - ya yi bayanin cewa wanda ya aikata haka, to, yana daga cikin mafi lalacewar mutane a wajen Allah.
- Sheikhul Islam Ibn Taimiyah - R.A - ya ce: Wadannan sun tattaro fitina biyu: Fitinar kaburbura da fitinar gumaka.
- [Ya zo] a cikin Sahihaini daga [Nana] A'isha - R.A - ta ce: yayin da aka sauko masa – ai mala'ikan mutuwa ya sauko masa- a wajen manzon Allah - SAW - sai ya rika dora wata rigarsa a fuskarsa, idan ya samu damuwa sai ya dauketa, sai ya fada yana cikin haka: **"La'antar Allah ta tabbata a kan Yahudawa da Nasara sun dauki kabarin Annabawansu a matsayin Masallatai" yana yin gargadi game da abin da suka aikata, daba don haka ba da an fito da kabarinsa , sai dai an jiye tsoron a dauke shi a matsayin masallaci".**
- Hakika Annabi - SAW - ya damu da wannan batun har sai da ya yi jan kunne game da hakan alhalin yana halin damuwa da kuma fitar rai, irin abin da ya ke nuna matsanancin tsoronsa a kan al'ummarsa a kan aikata irin abin da Yahudawa da Nasara suka aikata, sai su fada a cikin shirka kamar yadda suka fada.
- Hadisin yana nuni a kan cewa wanda ya aikata haka la'antacce ne, kamar yadda aka la'anci Yahudawa da Nasara.

---

1 - Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi.

- Ina sauran musulmai suke –Allah Ya shiryesu- game da wadannan hadisai!!
- Muslim ya rawaito daga Jundub dan Abdullahi - R.A - ya ce: **Na ji Annabi - SAW - kafin ya rasu da kwana biyar alhalin yana cewa: "Ku saurara, hakika wadanda aka yi kafinku sun kasance suna rikar kaburburan Annabawa a matsayin masallatai, Ku saurara kada ku riki kaburbura a matsayin masallatai, hakika ina hanaku yin haka"**.
- [Imam] Ahmad [yana da hadisi] da isnadi jayyid daga Ibn Mas'ud marfu'i: **"Lallai yana daga cikin mafi sharrin mutane su ne wadanda alkiyama za ta riskesu alhali suna raye, da wadanda suke rikar kaburbura a matsayin masallatai"**

## ➢ RIKAR KABUBURA A MATSAYIN MASALLATAI DA YA KASANCE DAGA CIKIN MANYAN ZUNUBAI DA HANYOYIN SHIRKA NAU'I BIYU NE:

1- A gina masallatan a kan kaburbura, a rika sallah a cikinsu domin girmamawa ga wanda ya ke kabarin, ko kuma don neman albarkarsa kamar yadda suke rayawa.

2- A yi sallah a wajen kaburburan ko da ba a gina masallacin ba.

- Duk wannan yana daga cikin hanyoyin shirka, ta hanyar girmama na kabarin, kamar yadda ake gani abin takaici, ta yadda suke shiga cikin khushu'I da kaskantar da kai, me yiwuwa ma su fuskanci kabarin su yi sallah raka'a biyu, wasu ma dawafi su ke yi a kabarin kamar yadda ake dawafi a dadadden daki [Ka'aba], wani daga cikinsu kuma yana kankame tagar kabarin yana neman tabarruki da ita, 'yan kadan ne cikinsu suke karanta fatiha ga ruhin wanda ke cikin kabarin , wannan yana daga cikin fararrun bidi'o'i.
- Hakika malamai daga dukkan mazhabobi sun yi Ijma'i a kan hana gini a kan kaburbura, da haramcinsa, da wajabcin rushe abin da aka gina a kansu na masallatai da kubbobi…
- Hana rikar kabubura a matsayin masallatai kuma yana nuni bisa haramcin sallah a cikinsu.

- Hana gina masallatai a kan kaburbura, abin da ya fi shiga wannan babin shi ne gina kubbobi a kai, da wuraren ziyara a kaburburan.

***Muna rokon Allah shiriya ga kowa…***

***Darasi na goma ya kare tare da godewa Allah…***

****

## (11)

## [MAULUDAI A MUSULUNCI]

### MAULUDAI:

- Su ne abubuwan da ake yi wa Annabawa da Waliyyai da Salihai a ranekun haihuwarsu na tarurruka da haduwa da abinci da sauransu …
- Domin girmamasu ko bayyanar da soyayyarsu ko neman tabarrukin zamani ko lokacin haihuwarsu da manufofi makamancin haka.
- Mauludai su kan kasance na zamani, kuma su kan kasance na wurare.
- Na zamani shi ne taron Mauludin Annabi ko Shehi a wani lokaci ayyananne.
- Na waje kuma shi ne taruwa don mauludinsa a wajen kabarinsa da daura da shi ta hanyar ziyararsa, aikata ayyukan mauludin sanannu ne a wajen masu yi.
- Dukkanin mauludai bidi’a ne a Musulunci, domin Annabi – SAW - bai taba yi wa kansa mauludi ba, kuma sahabbai ba su yi masa mauludi bayan wafatinsa ba, [Sayyidina] Abubakar - R.A - bai yi ba , ko [Sayyidina] Umar - R.A - ko [Sayyidina] Usman R.A, ko [Sayyidina] Aliyu - Allah ya yarda da su bakidaya -.
- Idan ya kasance ba su yi mauludi ba duk da kishinsu wajen yin aiki nagari, sai ya nuna cewa ba ya cikin addinin Musulunci.
- Imam Malik bn Anas Imam Dar Al-hijra - R.A - ya ce: Duk abin da bai kasance addini a wancan lokacin ba, ayau ba zai zama addini ba.
- Ai duk abin da bai kasance addini a zamanin manzon Allah – SAW - ba, to, a yau ma ba addini ba ne, saboda Allah - SWT - Ya kammala adddini da wafatin manzon Allah – SAW -, Allah – SWT - Ya ce: ***(A yau na cika muku addininku)***[1] … har karshen Aya.
- Farkon wadanda suka fara Mauludai su ne Ubaidiyyuna Rafilawa wadanda suka mulki Misra a iyalai na hudu.. kafin haka ba a san yin Mauludai ba ko mauludin manzon Allah - SAW - ko mauludan waliyyai da salihai.
- Shin sunnar rafilawa ka ke so ko kuma sunnar fiyayyen manzanni?

1 - Surat al-Ma’ida aya ta 3.

- Saboda haka ne ba za ka samu ambaton mauludin Annabi ko na waninsa a zancen limamai hudu ba, saboda ba a sanshi a zamaninsu ba.
- Annabi - SAW - ya ce: **“Ka da ku sanya gidajenku a matsayin kaburbura, kuma ka da ku sanya kabarina ya zama idi, ku yi min salati, hakika salatinku yana isa gareni a duk inda ku ka kasance”**[1].
- Idan Annabi - SAW - ya kasance ya hana a sanya wajen kabarinsa a matsayin idi da za a rika taruwa a cikinsa kamar yadda a ke yi yanzu a mauludan Hussain da na Badawiy da na Bura’iy da na Aidarus da na Shazaliy da na Sheikh Abdul-Kadir Jilani .. da sauransu, da abin da ya ke faruwa a cikinsu na shirka da bidi’o’i da raye-raye da cakudedeniya tsakanin maza da mata da lalacewar tarbiya.. da sauran abubuwan da ba sa buya ga kowa..
- Idan har Annabi - SAW - ya hana a yi masa idi [taron biki], to, hana yi masa irin wadannan mauludai ga wadanda ba su kai shi ba shi ne ma ya fi zama abin hanawar.
- Yana daga cikin barnace-barnacen mauludin Annabi da waninsa na sauran mauludai kasancewarsu idi ne na bidi’a, hakika Musulunci ba ya halatta wa idan ba idi guda biyu ba: Al-fitri [karamar Sallah] da al-Adha [babbar Sallah]..
- Mauludai idi [biki] ne akwai na lokaci da na wuri.
- Babu wani wanda ya ke da damar ya kebance wani lokaci ko wuri ya mayar da shi idi [biki], hakika wannan na Allah - SWT - ne Shi kadai, ba na [wani abin] halitta ba ne, Allah - SWT - ya ce: ***(Ubangijinka Shi ne Ya ke halittar abin da Yake so, kuma Yake zaba)***[2]. Allah - SWT - Shi ne wanda Ya halicci lokuta da wurare, kuma Shi ne Ya ke fifita wasu a kan wasu , kuma ya zabe su.
- Wanda ya ke raya cewa mauludai bidi’a ne mai kyau, to, hakika ya kaucewa daidai, kuma ya zo da abin ban mamaki, duk wanda zai kalli abubuwan da suke faruwa na munkari [barna], zai gane cewa ba wata bidi’a mai kyau, sai dai mummuna da barna da zur da bata.
- A musulunci babu bidi’a mai kyau , sai dai ma duk bidi’a bata ce , hakika Annabi - SAW - ya kasance yana fada a kan minbari a duk Juma’a **“ …**

---

1 - Abu Dawud ne Ya rawaito shi da isnadi mai kyau.
2 -Surat al-Kasas: Aya ta 68.

**duk kan bidi’a bata ce ..”** ita kuma “duk” tana daga cikin lafazai na gamewa , sai ta nuna cewa kowace bidi’a bata ce.

- Ka kiyaye ya dan uwana musulmi wajen halartar mauludai domin munkari ne, zur ne, kuma barna ne.
- Soyayyar Annabi - SAW - da soyayyar waliyyai tana kasancewa ne ta hanyar biyayyarsu ga sunnah da kuma kiyayar bidi’a.

***Muna rokawa kowa shiriya..***

***Darasi na goma sha daya ya kare tare da godewa Allah.***

****

## (12)

## (HUKUNCIN SIHIRI [TSAFI] A MUSULUNCI)

- Sihiri [Tsafi] yana daga cikin abubuwan da suke warware Musulunci; saboda mai tsafi ba zai zama mai tsafi ba sai idan ya kafircewa Allah – SWT -.
- Allah - SWT - Ya ce: ***([Annabi] Sulaiman bai yi kafirci ba, sai dai shaidanu ne suka yi kafirci, suna koyawa mutane tsafi)***[1].
- Sihiri yana daga cikin ayyukan Yahudawa, Allah - SWT - Ya ce game da su: ***(Sun yi imani da Jibti da Dagutu)*** Umar - R.A - ya ce: Jibti: Shi ne sihiri, Dagutu shi ne shaidan.
- Sihiri layu ne da wasu tawaida da kulle-kulle da suke tasiri a zukata da jiki, suna kisa suna raba tsakanin miji da matarsa.
- Wanda duk ya ke ta'amuli da shi , to, ba shi da rabo a lahira, kamar yadda [Allah] SWT Ya ce: ***(Lallai sun sani cewa duk wanda ya saye shi)*** - ai ya yi ta'amuli da shi , ya ke amfani da shi- ***(ba shi da kaso a lahira)***[2] ai rabo na rahamar Allah.
- [Manzon Allah] SAW ya ce: **"Ku nisanci abubuwa bakwai masu hallakarwa.. daga ciki ya ambaci: Sihiri"**[3].
- Ma'anar: Mubikaat: shi ne masu hallakarwa.
- Masu sihiri kafirai ne mutanen banza ne, ba sa kai wa ga sihirinsu sai bayan kafurci da shirka, sai shaidanu su umarce su da kafirci domin su kasance masu sihiri suka rika yi musu hidima.
- Yana daga cikin haka yi wa shaidanun sujjada, ko su wulakanta Al-Kur'ani ta hanyar jefa shi cikin wurare masu najasa, ko su rubuta shi da jini da najasa- Allah dai ya la'ance su- da sauran abubuwa masu datti da kazanta da suke aikatawa domin neman kusancin shaidanu domin su yi musu hidima.
- Sabo da haka hukuncin masu sihiri a musulunci shi ne kisa.
- An karbo daga Jundub [hadisi] marfu'I: **"Haddin mai sihiri shi ne duka da takobi [wato kisa]"**[1].

1 - Surat al-Bakara aya ta 102.
2 - Surat al-Bakara: Aya ta 102.
3 - Bukhari da Muslim ne suka rawaiti shi.

- Yana haramta a kan Musulmi ya tafi wajen masu sihiri da bokaye da masu rufa-ido domin neman neman magani, ko da mai sihirin ya yi da'awar shi yana cikin shehunai, kamar yadda wasu shehunan sufaye su ke da'awa.
- [Annabi] SAW ya ce: **"Wanda ya je wajen dan duba sai ya tambayeshi game da wani abu, to, ba za a karbi sallarsa ba ta kwana arba'in"**[2].
- [Annabi] SAW ya ce: **"Wanda ya je wajen boka sai ya gasgata shi cikin abin da ya ke fada, to, ya kafirce wa abin da aka saukar wa [Annabi] Muhammad SAW"**[3].
- Biya [karanta] tafin hannu da finjani da masu ramlu da masu yin duba cikin burujai da taurari duk kansu bokaye ne wadanda suke da'awar sanin gaibu.
- Tamabayarsu daidai ya ke da ziyararsu a wurarensu, ko tabhanyar kiran waya, ko bibiyarsu a tashoshi setlayit *[setlite]* duk kansu haramun ne ya shiga cikin narkon ya zo a hadisan da suka gabata.
- Gaibu babu wanda ya sanshi sai Allah, yana daga cikin kebance-kebancen *Rububiyyar* Allah SWT.
- Allah - SWT - Ya ce***: (Ka ce: Babu wanda ya san gaibu a sammai da kassai sai Allah)***[4].
- Har [Annabi] Muhammad - SAW - a rayuwarsa bai kasance ya san gaibu ba, Allah - SWT - Ya ce game da shi: ***(Da a ce na san gaibu da na yawaita alheri, da wani mummunan abu bai sameni ba)***[5].
- Wajibi a kan musulmi shi ne yi wa kai garkuwa da Azkaar da wurudai na shari'a domin Allah Ya tsare shi daga sharrin masu sihiri.
- Yana daga cikin hakan: Ayatul Kursiyyi, da gabadayan surat Al-bakara, da Kula-uzai.
- Ya kamata ga musulmi ya kasance a gidansa akwai litattafai na Azkaar, kuma ya haddace abin da zai iya daga ciki, daga ciki akwai:

1- Al-Azkaar na al-Nawawiy
2- Al-wabil al-sayyib na Ibn al-kayyim
3- Tuhfatul Akhyaar na Ibn Baz

---

1 Tirmiziy ne ya rawaito shi, ya ce Sahihiyar magana hadisin maukufi ne (maganar sahabi ce).
2 - Muslim ne ya rawaito.
3 - Abu-Dawud ne ya rawaito shi.
4 - Surat al--Naml: Aya ta 65
5 - Surat al--Aa'raaf: Aya ta 188.

4- Hisnul Muslim na Sa'id bn Wahb

Allah Ya yi musu rahama bakidaya.

- Kada mu manta da yi wa yara ta'awiza a safiya da maraice, idan yaro ya iya magana sai a sa shi ya haddace kula-uzai da Ayatul-kursiyyi, kuma a koya masa Bismillah a kowane hali.

***Muna rokon Allah Ya yi mana maganin sharrin masu sharri, da kaidin mutanen banza.. Allahumma Amin.***

***Darasi na goma sha biyu ya kare tare da godewa Allah.***

****

## (13)

## [ SOYAYYA A MUSULUNCI)

### SOYAYYAR ALLAH:

- Ita ce matsayin da masu gasa suke gasa a kanta, kuma wajen samunta ne masu tsere suke tsere, kuma a kanta ne masoya suke kure maleji, ita ce abincin zuciya, kuma abincin ruhi, kuma sanyin idanu.
- Ita ce asalin addinin musulunci wanda a kansa ne dutsen nikanta ya ke kewayawa, da kamalarta ne imani ya ke samun kamala, da tawayarta ne tauhidin mutum ya ke samun tawaya.
- A cikin addu'ar Annabi - SAW - : **"Ina rokonKa soyayyarKa da soyayyar wanda ya ke sonKa, da son aikin da zai kusantar da ni zuwa soyayyarKa".**
- Soyayyar Allah ita ce mafi darajar ibadu, ita ce soyayyar da take tabbatar da *Ubudiyya* [bauta] da kaskantar da kai, da risnawa da girmamawa, da kamalar da'a, da fifita Shi akan waninSa – SWT -.
- Irin wannan soyayyar da wannan siffar ba a yi wa kowa sai Allah – SWT-, wanda ya sarrfa wani abu na ta ga wanin Allah, to, ya yi shirka.
- Hakika Allah Ya ambata daga cikin shirkar mushirikai akwai soyayyar kishiyoyinsu soyayya mai daidai da ta Allah, Sai Allah - SWT - Ya ce: ***(Daga cikin mutane akwai wadanda suke rikar wasu kishiyoyi koma bayan Allah suna sonsu kamar son Allah)***[1] ai suna daidaita su da Allah wajen soyayya da girmamawa, kamar yadda suke aikatawa da gumakansu da ababen bautarsu cikin salihai da sauransu, sai suke bauta musu bauta ta soyayya da kaskantar da kai da risnawar da ba ta dace da kowa ba sai Allah – SWT -, shi ya sanya za ku fadawa ababen bautarsu alhali suna cikin wuta ***(Mun rantse da Allah lallai mun kasance cikin bata bayyananne, a lokacin da mu ke daidaita ku da Ubangijin talikai)***[2] ai cikin soyayya da ibada.
- Soyayya ta gaskiya ga Allah tana lazimta sanya abin son Allah - SWT - a gaban dukkan abubuwan son zuciya idan aka samu cin karo.

---

1 -Surat al-Bakara: Aya ta 165.

2 - Surat al-Zukhruf: Aya ta 97 – 98.

- [Allah] SWT Ya ce: [ Ka ce idan iyayenku da 'ya'yanku da 'yan uwanku da matanku da danginku da dukiyar da ku ka samu da kasuwancin da ku ke tsoron karyewarsa da wuraren zama da ku ke so sun kasance mafi soyuwa a gareku sama da Allah da manzonSa da yin Jihadi a tafarkinSa; to, ku jira har Allah Ya zo da al'amarinSa, Allah ba Ya shiryar da mutane fasikai][1].
- Soyayya ta gaskiya ga Allah - SWT - tana lazimtar biyayya ga [Annabi] Muhammad – SAW-, [Allah] SWT Ya ce***: (Ka ce: In kun kasance kuna son Allah, to, ku bi ni sai Allah Ya so ku, kuma Ya gafarta muku zunubanku, Allah Mai yawan gafara ne, Mai yawan jin kai ne)***[2].
- Soyayya ta gaskiya ga Allah - SWT - tana lazimtar gabatar da soyayyar manzon Allah - SAW - game da kowane abu ko da a kan kai ne, [Manzon Allah] SAW ya ce: **"Imanin dayanku ba zai cika ba sai na kasance mafi soyuwa a gareshi daga dansa da mahaifinsa da mutane bakidaya".**
- Wannan yana lazimtar gabatar da sunnarsa - SAW - a kan maganar kowa duk yadda ya ke da girma.
- Soyayya ta gaskiya tana lazimatar son imani da muminai, da kin kafirci da kafirai, [Allah] SWT Ya ce: ***(Ba za ka samu mutanen da suka yi imani da Allah da ranar lahira ba suna kaunar wanda ya yi fito-na-fito da Allah da manzonSa ba, ko da sun kasance iyayensu ko 'ya'yansu ko 'yan uwansu ko danginsu)***[3].
- Musulunci baya hana abubuwan da dan Adam yake ji na al'ada da kuma soyayya ta dabi'a, Hakika Annabi - SAW – ya kasance yana son kayan zaki da zuma, yana son matansa, mafi soyuwa a wajensa ita ce [Nana] A'isha - R.A -.
- Soyayyar mahaifa da 'ya'ya soyayya ce ta dabi'a da halitta.
- Soyayyar aminai da abokan aiki cikin musulmai soyayya ce ta dabi'a.
- Soyayyar mai jin yunwa ga abinci, da ta mai jin kishirwa ga ruwa soyayya ce ta dabi'a ba ta tasiri a cikin Tauhidi.

---

1 - Surat al-Tauba; Aya ta 24.
2 -Surat al-Imraan: Aya ta 31.
3 - Surat al-Mujadalah: Aya ta 22.

- Soyayyar dukiya da kasa soyayya ce ta halitta da dabi’a ba ta tasiri a Tauhidi, matukar ba a gabatar da ita a kan soyayyar Allah ba a lokacin samun cin karo.
- Mafi kwarin igiyar imani ita ce soyayya saboda Allah, da kiyayya saboda Allah.
- Masu yin soyayya saboda girman Allah suna kan mimbarai na haske a ranar alkiyama.

***Darasi na goma sha uku ya kare tare da godewa Allah.***

****

## (14)

## [TSORO A MUSULUNCI]

- Tsoro yana daga cikin mafi falalar mukamai a addini kuma mafi girmansu, hakika Allah Ya ambaceshi a littafinSa daga mala'iku makusanta da waliyyai da salihai.
- [Allah]SWT Ya ce: ***(Suna tsoron Ubangijinsu da ya ke samansu, suna aikata abin da ake umartarsu)***[1].
- [Allah]SWT Ya ce: ***(Kuma suna masu sauna ne saboda tsoronSa)***[2].
- [Allah]SWT Ya ce: ***(Wanda ya ji tsoron tsayuwa gaban Ubangijinsa yana da aljannatai guda biyu)***[3].
- [Allah]SWT Ya ce: ***(Hakan [sakamako ne] ga wanda ya ji tsoron tsayuwa gabaNa, kuma ya ji tsoron narkoNa)***[4].

**TSORON DA YA KE BIJIROWA MUTUM KALA UKU NE:**

- **NA FARKO: TSORO NA SHIRKA:**

- Shi ne tsoro na boye, shi ne mutum ya ji tsoron wanin Allah zai dora masa abin da Ya so na rashin lafiya ko talauci ko kisa da sauransu ta hanyar ikonSa da ganin damarSa.
- Shi ne irin wanda mushirikai suke kudirce shi ga abubuwan bautarsu..
- Kuma shi ne a yau masu bautar kaburbura suke kudirceshi a mamatansu, saboda wannan suke neman kusanci zuwa garesu ta hanyar addu'a da yanka da bakance saboda tsoronsu, da kuma fatan abin da ya ke wajensu –bisa rayawarsu-..
- Da za ka nemi dayansu ya yi rantsuwa da Allah da zai yi alhalin karya ya ke, idan kuwa ya kasance rantsuwa ce da na cikin kabarin daga cikin wadanda ya ke da akida a kansa ba zai rantse ba, ba don komai ba sai don wanda ya ke abinne a cikin kasa ya fi jin tsoronsa sama da Allah, Allah Ya tsare.
- Wannan nau'in na tsoro shirka ne mafi girma yana fitar da mai yinsa daga addinin Musulunci, Allah Ya tsare.

---

1 - Surat al-Nahl: Aya ta 50.
2 - Surat al-Anbiya: Aya ta 28.
3 - Saurat al-rahman: Aya ta 46.
4 - Surat Ibrahim: Aya ta 14.

- **NA BIYU: TSORO NA DABI'A:**

- Shi ne mutum ya ji tsoron wani abokin adawa ko zakoka da sauransu, wannan ba abin zargi ba ne, shi ne wanda Allah – SWT - Ya ambata game da [Annabi] Musa **[sai ya fito daga cikinta yana mai jin tsoro yana sauna]**[1].

- **NA UKU: MUTUM YA BAR ABIN DA ALLAH YA WAJABTA MASA NA DA'AR ALLAH DA NEMAN LADA SABODA TSORON MUTANE, WANNAN HARAMUN NE:**

- [Allah] SWT Ya ce: ***[Ai kadai dai wancan Shaidan ne yake tsoratar da masoyansa, kada ku ji tsoronsu, ku ji tsoroNa in kun kasance masu imani)***[2] ai yana tsoratar da ku game da masoyansa, yana sanya muku jin cewa za su iya yanke muku arzikinku, kuma cewa su suna da tsanani da karfi.

- **NA HUDU: TSORON NARKON ALLAH DA YA YI WA MASU SABO:**

- Shi ne wanda Allah Ya fada game da shi [ hakan [zai kasance] ga wanda ya ji tsoron tsayuwata ***[da shi] kuma ya ji tsoron narkoNa]***[3].
- [Allah] Ya fada game da shi: ***[Wanda ya ji tsoron tsayuwa gaban Ubangijinsa yana da aljanna biyu]***[4].
- Wannan tsoron yana daga cikin mafi girman matakan imani, shi ne wanda ya ke tsare musulmi daga aikata ayyukan sabo, shi da fata abokai ne [a tare su ke], ba za ka kai ga Allah ba sai da su [biyun], shi tsoron yana hana aikata sabo, fata kuma yana kwadaitarwa a kan aikata ayyukan da'a..
- Duk abin da ya karu a kan wannan, to, ba a bukatarsa …

***Gam katar ta tabbata ga Allah. Tsira da amincin su tabbata ga Annabimmu Muhammad.***

***Darasi na goma sha hudu ya kare tare da godewa Allah.***

****

---

1 - Surat al--kasas: Aya ta 21.
2 - Surat al-Imran: Aya ta 175.
3 - Surat Ibrahim: aya ta 14.
4 - Surat al-Rahman: Aya ta 46.

## (15)

## (DOGARO GA ALLAH)

- Dogaro ga Allah (tawakkali) shi ne dogaron zuciya gareShi, da fawwala al'amura gareShi, ba a fatan kowa sai Shi, kuma ba a nufar kowa sai dai Shi.
- Dogaro ga Allah shi ne mafi kololuwar mukaman Tauhidi, Allah Ya sanya shi sharadi ne na imani, sai [Allah] SWT Ya ce: ***[A gareshi kadai ku dogara in kun kasance Musulmai]***[1].
- Dogaro ga Allah yana daga cikin siffofin muminai, Allah - SWT - Ya ce: ***[Kadai dai muminai su ne wadanda idan aka ambaci Allah zukatansu suna raurawa, idan aka karanta musu ayoyinSa sai su kara musu imani, kuma ga Ubangijinsu ne kawai suke dogaro]***[2].
- Wanda ya dogara ga Allah, to, Allah Ya isar masa, ai ya isheshi, ba ya bukatar kowa a tare da shi.
- [Allah] SWT Ya ce: ***[Ya kai wannan Annabi, Allah Ya isar maka, da wadanda suke tare da kai daga cikn muminai]***[3].
- [Allah] SWT Ya ce: [***wanda Ya dogara ga Allah, to, Ya isar masa]***[4].
- [Malam] Ibn Al-Kayyim - R.A -: Ai Ya ishe shi, wanda duk ya zama Allah ne Ya isar masa, kuma Mai kareshi, babu wani kwadayi da makiyinsa zai yi masa, kuma ba zai cutar da shi da komai ba, sai dai abin da babu makawa a kansa kamar zafi da sanyi da yunwa da kishirwa..
- Dogaro ga wanin Allah wajen neman nasara da arziki da kariya shirka ne mafi girma, hakika wadannan al'amura suna daga cikin abubuwan da babu masu iko a kansu sai Allah.
- Wannan yana faruwa ne daga masu bautar kaburbura, hakika suna fakewa garesu domin neman tsari daga makiya, kuma suna neman nasara daga wajensu akan makiyansu.
- Kamar yadda wani mai magana daga cikinsu ya ke fada yayin da Tatar suka yaki Damaskas:

---

1 - Surat Yunus: Aya ta 84.
2 -Surat al-Anfaal: 2.
3 - Surat al-Anfaal: 64.
4 - Surat Al-talak: aya ta 3.

*Ya ku masu tsoron Tatar   ku fake da kabarin Abu-Umar*

*ku fake da kabarin Abu-Umar   zai tseratar da ku daga cuta*

**Muna neman tsarin Allah daga irin wannan shirka.**

- Wakilci halattacce shi ne ka wakilta mutum wajen biyan bukatar wani al-amari da ya ke da iko a kansa, wannan wakilci ne ba tawakkali ba.
- Dogaro ga Allah ba ya cika sai da aikata abin da Ya yi umarni da shi daga sabubba, Annabi - SAW - ya ce: **"Da a ce za ku yi tawakkali ga Allah hakikanin tawakkali da Ya azurtaku, kamar yadda Ya ke azurta tsuntsaye, su yi sammako su fita da yunwa, amma su maraita a koshe"** sai ya ambaci cewa suna yin sammako su fita, kuma su maraita.
- Mutanen Yaman sun kasance suna fita aikin hajji ba sa yin guzuri, suna cewa: Mu masu dogara ga Allah ne, idan suka zo Makka sai su rika rokon mutane, sai Allah - SWT - Ya saukar da: ***(Ku yi guzuri, hakika mafi alheri guzuri shi ne kiyayar Allah [Takawa]]***[1].
- Wani mutum ya zo wajen Annabi - SAW - sai ya ce: Ya ma'aikin Allah: taguwata shin in sanya mata dabaibayi ko kuma inyi tawakkali? Sai ya ce: Ka sanya mata dabaibayi sannan ka yi tawakkali" sai ya umarce shi da aikata sababi tare da dogaron zuciya ga Allah wajen tsare taguwarsa.

***Darasi na goma sha biyar ya kare tare da godiya ga Allah.***

****

1 - Surat al--Bakarah: Aya ta 197.

**(16)**

## (HAKURI DA KADDARAR ALLAH YANA DAGA CIKIN IMANI)

- Allah Ya hukunta bisa hikimarSa da adalcinSa Ya hukunta zai jarraba nau'in mutum da umarni da hani da musibu wadanda Ya kaddarasu a kansu.
- Kuma [Allah] SWT Ya umarcemu da hakuri bisa kaddararSa mai radadi kamar talauci da rashin lafiya da hadarurruka da mutuwa..
- Sai [Allah] SWT Ya ce: ***[Ya wadanda suka yi imani ku yi hakuri]***[1].
- Sai [Allah] SWT Ya ce: ***[Ka yi hakuri, hakurinka bai kasance ba sai sabo da Allah]***[2].
- Ya yi wa masu hakuri alkawari na lada gwaggwaba sai ya fada a cikin *Muhkam Al-Tanzil* [Al-Kur'ani]: ***[Kadai dai yana cikawa masu hakuri sakamakonsu ne ba tare da hisabi ba]***[3].
- Annabi - SAW - ya ce: **"Hakuri haske ne"**[4].
- Annabi - SAW - ya ce: **"Ba wanda aka bai wa kyauta mafi alheri mafi yalwa sama da hakuri"**[5].

### 🕮 HAKURIN DA AKA YI UMARNI DA SHI KALA UKU NE:

1- Hakuri a kan da'ar Allah.
2- Da hakuri da barin sabawa Allah.
3- Da hakuri a kan kaddarar Allah mai radadi.

### 🕮 HAKURI A KAN KADDARAR ALLAH MA'ANARSA [SHI NE]:

- (Tsare zuciya ga barin raki, da [tsare] harshe ga barin kai kara, da [tsare] gabbai daga abubuwan da Allah Ya haramta).
- Idan aka dorawa mutum wata masifa, to, lallai ne ya yi hakuri, hakurin wajibi ne, yarda kuma mustahabbi ce, ita din mataki ce babba a imani.

---

1 Surat al--imran: Aya ta 200.
2 - Surat al--Nahl: Aya ta 127.
3 - Surat al--Zumar: Aya ta 10.
4 - Muslim ne ya rawaito shi.
5 -Bukhari da Muslim ne suka rawaito.

## 🕮 DAGA CIKIN ABIN DA YA KE CIN KARO DA HAKURI AKWAI:

1- Dukan kumatu, da yaga aljihuna da kururuwa.

2- [Annabi] SAW ya ce: **"Wanda ya ke dukan kumatu ya ke yaga aljihu, ya ke yin addu'a da addu'ar Jahiliyya ba ya cikimmu".**

- [Annabi] SAW ya ce: **"Abubuwa guda biyu akwai kafirci a tattare da su: Sukar nasaba, da ihu akan mamaci".**

## 🕮 MA'ANAR NIYAHA [IHU]:

- Ai [yana nufin] daga murya da raki ta hanyar lissafo halayen mamaci.
- Amma kukan da babu daga sauti, baya cikin wanda aka hana.

3- [Annabi] SAW ya barranta daga mai aske kanta –ita ce wadda take aske kanta saboda masifa -da Mai raki- ita ce wadda take daga murya da kuka- da Mai yagawa- ita ce wadda ta ke yaga tufafunta don ta yi bayanin bakin cikinta game da mamaci..

- Barrantarsa - SAW - daga wadannan yana nuni a kan cewa aikinsu yana daga cikin manyan zunubai.
- An shara'anta wa mumini idan ya fada a masifa ya ce: "Mu daga Allah muke, kuma zuwa gareShi za mu koma, ya Allah Ka ba ni lada a cikin masifata, Ka musanya min da mafi alheri daga gareta.
- An sunnata yin ta'aziyya (jaje) ga wanda masifa ta same shi da fadar: Allah Ya kyautata ta'aziyyarka, Ya girmama ladanka, Allah Ya doraka (Ya baka karfin gwuiwa) game masifar da ta sameka, Allah Ya gafarta wa mamacinka…
- An sunnanta yin abinci ga Ahlin mamacin domin sassauta musu, da kuma karfafa gwuiwa a kan masifar da ta samesu, hakika [Annabi] SAW ya ce: **"Ku yi abinci ga iyalan Ja'afar hakika abin da zai dauke musu hankali ya samesu".**
- Yana daga cikin bidi'a kafa rumfuna da taruwar mutane a cikinta domin karbar ta'aziyya da yin abincin ga masu yin ta'aziyya.
- Ana yi wa wanda masifa ta sama ta'aziyya a kowane waje, a gidansa ko masallaci ko a wajen aikinsa da makamancin haka.

- Babu hani (laifi) waliyyan mamaci su taru a gidan dayansu domin a saukakawa masu yin ta’aziyya, ba tare da abubuwan da za su nuna yin raki ba.

***Darasi na goma sha shida ya kare tare da godewa Allah.***

****

**(17)**

## (RIYA TANA DAGA CIKIN SHIRKA)

### RIYA:

- Shi ne bawa ya aikata wani aiki nagari don mutane su gani su yaba masa, an tsago shi daga gani, sabo da mai yi don a gani, yana son mutane su ganshi ne.
- Riya tana daga cikin dabi'un munafikai, Allah - SWT - Ya ce: [***Hakika munafikai suna yaudarar Allah , Shi kuma Yana mayar musu da sakamakon yaudararsu, idan suka tashi yin sallah sai su tashi suna masu kasala, suna yi domin mutane su gani, ba sa ambaton Allah sai kadan]***[1].
- Wajibi ne a kan bawa ya rika nufar Allah - SWT - da aikinsa, idan ba haka ba ba za a karbi aikinsa ba ko da mai yawa ne, Allah - SWT - Ya ce: ***[Wanda ya ke fatan haduwa da Ubangijinsa (lami-lafiya), to, sai ya yi aiki nagari, kuma kada ya yi tarayya da kowa a tare da Shi]***[2].
- Daga Abu Sa'id [hadisi] marfu'I **"shin ba na ba ku labarin abin da na fi jiye muku tsoro ba sama da Masihu dujal? sai suka ce: Eh, sai ya ce: Boyayyar shirka, Mutum zai tsaya ya yi sallah, sai ya kawata sallarsa saboda mutane suna kallonsa"**[3].
- Kadai dai riaya ta kasance mafi abin jiye tsoro a kan salihai sama da Masihu Dujal, saboda buyanta, da kuma karfin abin da ya ke jawo yinta, da wuyar kubuta daga ita.
- Da kuma kasancewar Shaidan yayin da ya yanke tsammanin salihai ba za su daina aiki ba, to, sai ya ke son bata musu shi da riya.
- [Ya zo] a cikin Hadisi Kudusini: **"Nine mafi wadatar mafi wadatar abokan tarayya game da tarayyar, wanda ya aikata wani aiki da ya hadaNi da wani a cikinsa, to, zan bar shi da shirkarsa"**[4].
- Idan musulmi ya shiga aiki nagari yana mai ikhlasi don Allah – SWT -, sannan sai niyyar riya ta fado masa, to, idan ya tunkudeta, ya yaki Shaidan, to, ya samu lada bisa yakarsa da ya yi, da tunkudewa.

---

1 - Surat al--Nisa: Aya ta 147.
2 - Surat al--Kahf; Aya ta 110.
3 - Ahmad ne ya rawaito.
4 - Muslim ne ya rawaito shi.

- Idan kuma ya saki jiki tare da riyar aikinsa da ya hada da riyar zai lalace, ya yi saɓo a dalilinsa.
- Mai riya yana da raunin zuciya, ta yaya zai rika yi don a gani ga wanda ba ya ba da lada ko ukuba!
- Mai riya kamar matafiyi ne wanda ya cika burgamensa da rairayi, sai yayi masa nauyi, kuma ba zai amfaneshi ba.
- Mai riya , riyarsa ta bayyana ga mutane, kamar yadda aka ce:

*Tufafin riya yana bankade abin da ya ke kasansa*

*Idan dai ka rufa da shi, to, ka sani a tsairara ka ke*

- Riya shirka ce karama idan dalilinta karami ne, amma idan ya kasance da yawa, to, mai riyar ya sani aikinsa yana rikidewa ba don Allah ba, sai ya zama shirka mafi girma.

***Muna rokon Allah lafiya da zaman lafiya.***

***Darasi na goma sha bakwai ya kare tare da godewa Allah.***

****

**(18)**

## [DANGANTA NI'IMOMI GA WANIN ALLAH YANA DAGA CIKIN SHIRKA)

- Yayin da ya kasance Allah - SWT - Shi ne mai yin ni'ima ga halittarSa ta zahiri da ta boye, kamar yadda Ya fada game da kanSa: ***(Duk abin da ku ke da shi na ni'ma, to, daga Allah ne)***[1] . Kuma Ya ce: ***(Ya zuba muku ni'imominSa na zahiri da na badini)***[2].
- Ya zama lallai a kan bawa ya yarda da falalar Ubangijinsa da Ya yi masa sai ya gode a kanta, daga cikin gode mata akwai raɓata zuwa ga majiɓincinta wanda Ya yi ni'ima da ita – SWT -.
- [Allah] SWT Ya ce: ***(Sun san ni'imar Allah sannan kuma suke musanta ta)***[3].
- Mujahid ya ce: Shi ne mutum ya ce: Wannan dukiya ta cena gajeta daga iyayena.
- Ai idan aka tuna masa ni'imar dukiya sai ya manta wanda ya yi masa ni'ima da ita, wanda Shi ne Allah, sai ya danganta ga iyayensa wadanda ya gaji dukiya daga wajensu.
- Sai Allah - SWT - Ya kira wannan da inkarin ni'ima.
- Awn bn Abdullahi ya ce: Suna cewa: Da ba don wane ba, da kaza bai faru ba.
- Danganta ni'ima ga wani, da manta Allah - SWT - ana daukarsa a matsayin inkari da musun ta.
- [Allah] Ya ce: ***(Kada ku sanya wa Allah kishiyoyi alhali kuna sane)***[4].
- Ibn Abbas: Ya ce: Shi ne fadinsu: da ba don karyar wane ba, da barayi sun zo mana, da ba don agwagwar cikin gidan ba; da barayi sun zo mana, da fadin mutum: da ba don Allah  da wane ba , kar ka sanya (wane) a ciki, duk wannan shirka ne.

---

1 - Surat al-Nahl: Aya ta 53.
2 - Surat Lukman: Aya ta 20.
3 - Surat al-Nahl: Aya ta 83.
4 -Surat al-Bakarah: Aya ta 32.

- Sheikh Ibn Uthaimin - R.A -: Kada ka ce: Da ba don Allah da wane da ya tsamoni ba; da na nitse, ba ya halatta, domin ka sanya sababi abin halitta ya yi daidai da halitta sababin, wannan nau'i ne na shirka.
- Daidaita abin halitta da Mahalicci wajen danganta ni'imominSa gareshi shirka ne, kamar yadda Ibn Abbas - R.A - sai dai yana cikin shirka karama, ita ce shirkar lafazai.
- Da ya ce: Da ba don Allah Shi kadai ba; da na nitse, wannan ya fi kamala, idan kuma ya ce: Sannan wane da na nitse, lallai wannan ya halatta, saboda (sannan) tana nuna jerantawa da biyo baya tare da jinkiri… sai ka tabbatar da ni'ima ga Allah, ka sanya abin halitta bayan Allah – SWT -.
- Takaitacciyar magana ita ce ya wajaba a yi ladabi tare da Allah wajen danganta ni'imomin gareShi.
- Idan aka ce da kai: Ta yaya ka ci jarrabawa? Sai ka ce wannan yana daga cikin falalar Allah da Ya yi mini, kada ka ce da kokarina da dagewata, idan ka so ka ce: Wannan da falalar Allah ne sannan da dagewata.
- Idan ka warke daga rashin lafiya kada ka ce: Wannan falalar likita wane ce, sai dai ka ce: Wannan da falalar Allah ne Shi kadai, in ka so ka ce: Da falalar Allah - SWT - sannan likita.
- Idan Allah Ya tseratar da kai daga hadarin mota, kada ka ce saboda ni na kware wajen tuki sai na sarrafata, sai dai ka ce: Falalar Allah ce kai kadai.
- Sababin da abubuwan da aka sabbaba Allah - SWT - ne ya haliccesu.. kowane abu da falalar Allah- SWT - ne da karamcinSa.

***Darasi na goma sha takwas ya kare tare da godewa Allah*.**

****

**(19)**

## [ RANTSUWA DA WANIN ALLAH YANA DAGA CIKIN SHIRKA]

### KA SANI YA DAN UWANA MUSULMI:

- Tabbatar da Tauhidi ba ya cika sai da kiyayewa daga shirka kadan dinta da mai yawanta, har ma a cikin lafazai, ko da mai magana bai nufi ma'anar da ba ta halatta ba.
- Yana daga cikin hakan: Yin rantsuwa da wanin Allah – SWT -.
- Hakikar abin nufi da rantsuwa: Karfafar abin da aka rantse a kansa ta hanyar ambaton wani abu mai girma a tsakanin bangarorin biyu mai rantsuwa da wanda za a rantsewa,,, babu wani mai girman Allah – SWT -.
- [Allah] SWT Ya ce: ***(Kada ku sanya wa Allah kishiyoyi alhali kuna sane)***[1].
- Ibn Abbas - R.A - ya ce: Shi ne ka ce: Na rantse da Allah da rayuwarki ya wance, na rantse da rayuwata.
- Ai yin rantsuwa da rayuwar wani abin halitta, ana daukarsa a matsayin rikar kishiyoyi ne tare da Allah.
- Annabi - SAW - ya ce: **"Wanda ya rantse da wanin Allah hakika ya kafurta ko kuma ya yi shirka"**[2].
- Daga Buraidah [a hadisi] Marfu'I: **"Wanda ya rantse da amana ba ya cikimmu"**[3].
- Daga Abdullahi dan Umar - R.A - lallai Manzon Allah - SAW - ya riski Umar dan Khattab alhali yana tafiya a wani ayari yana rantsuwa da babansa, sai ya ce: **"Ku saurara! Lallai Allah Ya hanaku yin rantsuwa da iyayenku, wanda zai rantse, to, ya rantse da Allah ko kuma ya yi shiru".**
- A wata riwayar Umar ya ce: Na rantse da Allah ban sake rantsuwa da shi ba tun da na ji Annabi – SAW- ina sane [a kai na] ko hakaitowa [a madadin wani]".
- Ibn Abdil-Barr - R.A - daga cikin malaman Malikiyya ya ce: Ba ya halatta a rantse da wanin Allah bisa ijma'in malamai.

---

1 - Surat al--Bakara: Aya ta 32.
2 -Tirmiziy ne ya rawaito shi.
3 -

- Ibn Mas'ud - R.A - ya ce: 'Gwamma in rantse da Allah bisa karya shi na fi so, a kan in rantse da waninSa bisa gaskiya".
- Dalilin haka shi ne rantsuwa da Allah Tauhidi ne, ko da bisa karya ne, rantsuwa da waninSa shirka ne, ko da bisa gaskiya ne.
- Ladan Tauhi ya fi ladan gaskiya girma, zunubin karya ya fi sauki a kan zunubin shirka.
- A cikin *athar* din ibn Mas'ud da ya gabata a kwai dalili a kan cewa karamar shirka ta fi babban zunubi.
- Rantsuwa tana kasancewa da Allah ne da sanannun *adawaat* na rantsuwa (haruffan da ake rantsuwa da su): *Wawun* da *Ba'un* da *Ta'un*.
- Rantsuwa da wanin Allah ba tare da girmama abin rantsuwar ba, sai dai kawai wani abu da harshen mutum ya saba fada, kamar wanda yake rantsewa da babansa ko matsayinsa ko amanarsa ko (gashin bakinsa) shirka ce karama.
- Rantsuwa idan ta hadu da girmama abin da ake rantsewa da shi kamar yadda masu bautar kabari su ke yi, idan ka nemi ya rantse da Allah zai yi maka abin da ka ke so ko yana da gaskiya ko ba shi da ita, idan kuma ka nemi ya yi rantsuwa da shehu ko kasarsa ko rayuwarsa ba zai rantse ba idan ba shi da gaskiya.. to, wannan shi ne shirka mafi girma babu kokonto; saboda abin da aka rantse da shi an fi tsoronsa , an fi ganin girmansa, an fi girmamashi sama da Allah.
- Yana daga cikin rantsuwa da wanin Allah: Yin rantsuwa da Annabi - SAW - kamar ya ce: Na rantse da Annabi ban aikata kaza ba..
- Haka nan rantsuwa da rayuwar Annabi – SAW -, kamar ya ce: Na rantse da rayuwar Annabi.. duk wannan haramun ne ba ya halatta, kai! Yana cikin shirka.
- Yana daga irinsa yin rantsuwa da rayuwar mutum, kamar ya ce: Na rantse da rayuwata ban aikata kaza ba…
- Ko rantsuwa da darajar uwa, kamar ya ce: Na rantse da darajar uwata.
- Yana daga irinsa yin rantsuwa da Ka'aba, kamar ya ce: Na rantse da Ka'aba.
- Yana daga irinsa yin rantsuwa da kansa, kamar ya ce: Na rantsa da kai na abu kaza bai faru ba.

***Mutum mai Tauhidi ya kiyayi shirka kadan da mai yawa..***

***Darasi na goma sha tara ya kare tare da godewa Allah.***

****

## (20)

## [ HUKUNCIN SHU'UMANCI A MUSULUNCI]

- Yayin da shu'umanci ya kasance yana daga cikin akidu na masu shirka kamar yadda Allah - SWT - Ya ambata ga me da Fir'auna da mutanensa: ***[Amma yayin da daddaɗan abu ya zo musu, sai su ce: "Da ma wannan namu ne." Idan kuma mummunan abu ya same su, sai su camfa [Annabi] Musa da waɗanda suke tare da shi. Ku saurara, kawai dai mummunan abin da ya same su daga wajen Allah ya ke, amma yawancinsu ba sa sanin (haka)]***[1].
- Allah - SWT - Ya hana yinsa, ManzonSa - SAW - ya bayyana cewa babi ne daga babuka na shirka, sai ya ce: **"Camfi shirka ne, camfi shirka ne"**[2].
- Camfi shi ne yin shu'umanci da tsuntsaye, wannan sunan ya yi rinjaye a kan yin shu'aumancin saboda yawancin sha'umancin Larabawa suna yi ne da wasu tsuntsaye kamar mujiya da hankaka.
- Ya kasance yana daga jahilcin Larabawa idan suka yi nufin wani aiki muhimmi kamar yaki da makamancinsa, sai su tafi wajen taruwar tsintsaye su tashe su, idan suka yi dama sai su yi fatan nasara, idan kuma suka yi hagu sai su yi shu'umanci da su.
- Sai Musulunci ya zo ya bata wannan, sai Annabi - SAW - ya bayar da labari cewa wani abu ne a zuci da ba shi da tabbas a aikace, kamar yadda ya ke a hadisin Mu'awiya dan al-Hakam ya ce: Kuma daga cikimmu akwai mazaje masu yin camfi? Annabi - SAW - ya ce: **"Wannan wani abu ne da suke samunsa a cikin kirjinsu, amma ba zai hana su ba".**
- Hakika Annabi - SAW - ya kore camfi, sai ya ce: **"Babu daukar cuta, babu camfi, babu mujiya babu Safar"**[3].
- Duk abin da mutane za suyi shu'umanci da shi . to, yana daga cikin halittun Allah – SWT -, ba sa kawo alheri ko sharri, babu wani arziki a ciki ko tsiya..

---

1 - Surat al-A'raaf: 131.
2 - Abu Dawud da Tirmiziy ne suka ruwaito shi kuma ya inganta shi.
3 -Bukhari da Muslim ne suka rawaito.

- Daga cikin mutane akwai masu shu'umanci da wasu tsuntsayekamar mujiya da hankaka, idan ya sauka,  a gidansa sai ya ce: Ya kawo min labarin mutuwata.
- Daga cikinsu akwai wadanda suke shu'umanci da wasu watanni kamar Safar, da daura aure a Shawwal , da ranar Laraba a mako.
- Daga cikinsu akwai wadanda suke shu'umanci da wasu lambobi kamar lamba goma sha tara ko kuma goma a wajen Rafilawa.
- Daga cikinsu akwai wadanda suke shu'umanci da mai ido daya da gurgu a cikin mutane da sauransu cikin masu tawaya (nakasa).
- Da sauran wancanenku cikin abubuwan da ake samun sabani daga lokaci-zuwa-lokaci da kuma yanayin mutane.
- Wanda ya dogara ga Allah , ya tuno cewar alheri da kawar da sharri a hannunSa - SWT - ya ke, to, zai datse duk wata igiyar camfi daga zuciyarsa kafin ta samu tabbata.
- Wanda kuwa ya sakar mata da ragama ya damu da ita, to, za ta yi gaggawa zuwa gareshi sama da ruwa mai gangarowa zuwa magangarарsa, sai kuma kofofin waswasi su bude masa cikin abin da ya ji ya ke gani kuma ake ba shi.
- Shi camfi munana zato ne ga Allah , da kuma tsammanin saukar bala'i.
- Saboda da wannan ne Annabi - SAW - ya koyar da *fa'alu* (fata na gari), a maimakon camfi, sai ya ce: **“Babu daukar ciwo babu camfi, *fa'alu* (fata na gari) yana burge ni, sai suka ce: Menene *fa'alu?* Sai ya ce: “Kyakkyawar kalam”**.
- Malamai suka ce: Kaɗai dai Annabi - SAW - ya kasance *fa'alu* yana burgeshi, saboda shu'umanci munana zato ga Allah ne ba tare da wani dalili tabbatacce ba, shi kuwa *Tafa'ul* kyautata zato ne a ga Shi.
- Daga Anas **“Lallai Annabi - SAW - ya kasance idan ya fito domin bukatarsa yana son ya ji [ana ce wa] ya mai nasara, ya masanin hanya”**[1], wannan yana daga cikin fata na gari da mutum ya ke so ya ji.
- Idan mutum ya ji wani abu da ba ya so a zuciyarsa na camfi, sai ya ce: Ya Allah babu mai zuwa da kyawawan abubuwa sai Kai, babu mai kawar da mummuna sai Kai, babu tsimi babu dabara sai a wajenKa.

1 - Tirmiziy ne ya rawaito shi.

- Ahmad ya rawaito a hadisin Ibn Amr **"Wanda camfi ya sa ya fasa wata bukatarsa, to, ya yi shirka, sai suka ce: Menene kaffarar hakan? Sai ya ce: Shi ne ka ce: Ya Allah babu wani alheri; sai alherinKa, babu wani camfi sai camfinKa, babu abin bauta [da gaskiya] sai Kai"**.

***Darasi na ashirin ya kare tare da gode wa Allah.***

****

**(21)**

## [ HUKUNCIN IZGILI DA ADDINI KO SUNNA)

- Babu kokonto cewa imani da Allah da ManzonSa da addininSa ba sa haduwa da tare da izgili da addininSa da shari'arSa da sunnar manzonSa – SAW -.
- Hakika Allah - SWT - Ya hana yin izgili da addininSa sai Ya ce: ***[Ka da ku riki ayoyin Allah abin izgili)***[1].
- Saboda wannan Allah - SWT - Ya yi hukunci a kan masu izgili ga [Annabi] Muhammad da sahabbansa da cewa: ***(Ka ce: Yanzu da Allah ne ayoyinSa da ManzonSa ne kuka kasance kuna izgili. Kada ku ba da uzuri; hakika kun kafirta bayan imaninku)***[2].
- Hakan [ya kasance ne] bisa cewar wasu munafikai a yakin Tabuka sun taru suna tattaunawa suna cewa: "Ba mu taba ganin irin wadannan makarantan namu ba, mayun ci [masu yawan cin abinci], ko mafiya karyar harshe ba, ko mafi yawan ragwanta ba a lokacin haduwar [yaki] ba.. suna nufin Manzon Allah - SAW - da sahabbansa makaranta, sai Allah Ya saukar da wannan ayar.
- Izgili ga Allah ko addininSa mai yi da gaske da mai yi da wasa duka daya ne; saboda masu izgili sun kasance suna bayar da uzuri suna cewa: ***[Kadai dai mun kasance muna kutsawa ne muna wasa)***[3] ai ba da gaske mu ke ba, tare da haka Allah – SWT - bai yi musu uzuri ba.
- Yana daga cikin izgili: Wani ya yi da'awar cewa shari'ar Musulunci ba ta dace da aiwatarwa ba a wannan zamanin, cikin yin haka akwai raini da wulakanci ga shari'ar Allah - SWT - a cikin zuciyar mai wannan maganar.
- Yana daga cikin izgili ga addini: Yin nizgili ga sunnar Annabi - SAW - wajen cika gemu, ko daukarsa a matsayin mai dakile aiki da sana'antarwa.
- Yana daga cikin izgili ga addini: Yin izgili da sunnar Annabi – SAW - wajen dage tufafi saman idon sahu da daukar hakan a matsayin tsattsauran ra'ayi da tsanantawa da makamancinsa.

---

1 - Surat al--Bakarah: aya ta 231.
2 - SurataAl-Taubah: Aya ta 65 – 66.
3 - Surat al-Taubah: Aya ta 65.

- Yana daga cikin izgili ga addini: Yin izgili ga hijabin mace musulma, da kuma cewa dabaibaye mata ‘yancinta ne, kuma zai hanata sakat wajen aiki da sana’antarwa, ko kuma shi din koma baya ne da gargajiyanci, da makamantan wadannan kalamai na karya da saɓo.
- Yana daga cikin izgili ga addini: Izgili ga malamai da masu kawo gyara domin wulakantasu ta hanyar zane na *cartoon* da yake nuna su a yanayi mummuna kuma abin dariya.
- Yin izgili ga Annabwa da masu kawo gyara ita ce hanyar makiya manzanni tun a da, Allah - SWT - Ya ce***: [Hakika an yi izgili gawasu manzanni kafinka sai abin da masu izgilin suke ya tabbata a kansu)***[1].
- Allah - SWT - Ya ce: ***(Lallai wadanda suka yi manyan laifuka sun kasance suna yi wa wadanda suka yi imani dariya (a duniya). Kuma idan suka wuce ta wajensu sai su rika zunden su)***[2].
- Idan abubuwa suka tabbata ‘yan aljanna suka shiga aljanna, ‘yan wuta [suka shiga] wuta, anan ne asararre zai bayyana daga wanda ya ci riba, Allah - SWT - Ya ce: ***(Wannan shi ne sakamakonsu, Jahannama, saboda kafircewa da suka yi suka kuma riki ayoyiNa da manzanniNa abin yi wa izgili)***[3].
- Yana wajaba a kan musulmin da ya ke da tsoro game da imaninsa kada ya zauna tare da masu izgili kada ya yi hulda da su, saboda wanda ya yarda kamar wanda ya aikata ne, Allah - SWT - Ya ce: ***(Kuma idan ka ga wadanda suke kutsawa cikin ayoyinmu (suna izgili), to, ka rabu da su, har sai sun canja wani zancen da ba wannan ba)***[4].

***Darasi na ashirin da daya ya kare tare da godewa Allah.***

****

1 - Surat al-Biya: Aya ta 41.
2 - Surat al-Mutaffifin: Aya ta 29 – 30.
3 - Surat al-Kahfi: Aya ta 106.
4 -Surat al-An’am: aya ta 68.

## (22)

## [ABIN DA YA ZO GAME DA YAWAN RANTSUWA)

- Yayin da ya kasance manufar rantsuwa ita ce karfafa abin da aka rantse a kansa ta hanyar ambaton abu mai girma shi ne Allah – SWT-.. hakika Allah - SWT - Ya hana yawan rantsuwa da Shi domin wanzar da girmanSa a zukata.
- Allah - SWT - Ya ce: ***(Ku kiyaye rantsuwarku )*** Ibn Abbas - R.A - ya ce: Yana nufin kada ku rantse.
- Yawaita rantsuwa yana lazimta yawan kari, tare da abin da ya ke nunawa na rainuwa da rashin girmama Allah – SWT -.
- Daga Abu Huraira - R.A - ya ce: Na ji manzon Allah - SAW - yana cewa: **"Rantsuwa tana ciyar da haja, tana shafe [albarkar] nema"**[1]. Abin nufi shi ne rantsuwa ta karya tana ciyar da haja ta haɓaka ta sai dai yana zama dalilin shafewar albarkar neman.
- Daga Salman cewa Manzon Allah - SAW - ya ce: **"[mutum] uku Allah ba zai yi musu magana ba, kuma ba zai tsarkake su ba, kuma suna da azaba mai radadi: Tsoho mazinaci, da talaka mai girman kai, da mutumin da ya mayar da Allah hajarsa, ba ya saye sai da rantsuwarsa, kuma ba ya shiyarwa sai da rantsuwarsa"**[2].
- Wannan ne narko mai tsanani a hakkin wadannan, daga cikinsu akwai wanda ya mayar da rantsuwa da Allah ta lazimce shi, yawanci a halin sayarwa da saye, duk lokacin da ya so zai siya sai ya rantse, idan yana so ya siyar sai ya rantse, wannan ya nuna raunin Tauhidin wannan bawa, duk abin da ya ke cikin zuciya a harshe ya ke bayyana.
- Ibrahim al-Nakha'iy ya ce: Sun kasance suna dukanmu a kan shaida da alkawari alhalin muna kanana.
- Ai magabata sun kasance suna tarbiyyantar da yaransu a kan barin shaida da rashin kulla alkawari – alkawari da ma'anar rantsuwa- alhali suna yara, don a samu haɓakar girmama Allah - SWT - a zukatansu, da kuma rashin yin sakaci wajen yin rantsuwa da Shi.

---

1 - Bukhari da Muslim ne suka rwaito.
2 - Dabarani ne ya rawaito shi.

- Yana daga cikin wannan babin yawaita rantsuwa da saki a duk lokacin da ya so aikata wani abu, a cikin yin haka akwai raina haddodin Ubangiji da ayoyinSa.
- Allah - SWT - Ya fada bayan ambaton saki [***sai Ya ce]:[Kada ku riki ayoyin Allah ababen yi wa izgili]***[1].
- Ayoyin Allah su ne umarninSa da haninSa.

***Darasi na ashrin da biyu ya kare tare da godewa Allah***

****

1 - Surat al-Bakara: Aya ta 231.

## (23)

## [ HUKUNCIN ILIMIN TAURARI A MUSULUNCI)

### ILIMIN TAURARI:

- Shi ne ilimin sanin Taurari, Ma'anarsa kuma ita ce: Kafa dalili da yanayin falaki wajen abubuwan da suke faruwa a duniya.

### ILILIMIN TAURARI KALA UKU NE:

- **NA FARKO:** wanda ya kasance kafirci ne bisa *ijma'in* musulmai, shi ne kudirce cewa dukkan samammun abubuwa a duniyar ƙasa suna haduwa daga tasirin taurari, su kuma taurarin su suke aiki bisa zabin kansu, wannan ita ce mazhabar *Sabi'awa* 'Yan taurari wadanda aka aiko musu [Annabi] Ibrahim Badaɗayi - A.S -.
- **NA BIYU:** Kafa dalili a kan abubuwan da suke faruwa a ƙasa ta hanyar tafiyar taurari da haduwarsu da rabuwarsu da makamancin haka, suna cewa lallai hakan [yana faruwa ne] bisa kaddarawar Allah da ganin damarSa, babu tantama bisa haramcin hakan, saboda Allah - SWT - bai sanya wadannan ababen halitta a matsayin dalilin haka ba.
- **NA UKU:** Sanin masaukan rana da wata domin kafa dalili da hakan game da alkibla da lokatan sallah da lokatan shekara da sauransu.
- Wannan bangaren wasu malamai sun *karhanta* shi saboda tsoron zarcewa cikin wadannan ilimai.. wasu kuma sun yi rangwame kamar [imam] Ahmad da Ishaƙ.
- [Malam] Qatadah ya ce: Allah Ya halicci wadannan taurari ne saboda abubuwa uku: Yi wa sama ado, Jefe shaidanu, alamomin gane hanya, duk wanda ya yi wani tawili a kansu ba hakan ba, to, ya yi kuskure, kuma ya yi asarar rabonsa, kuma ya dorawa kansa abin da ba shi da iliminsa.
- Allah - SWT - Ya ce: ***[Hakika mun yi wa sama ado da fitilu (taurari), mun sanyasu ababen jefe shaidanu)***[1].
- Allah - SWT - Ya ce: ***[Da kuma alamomin [hanya]. Da kuma taurari ne suke gane [inda suka dosa])***[2].

1 -surat al-Mulk: Aya ta 5.
2 - Surat al-Nahl: Aya ta 16.

## 🕮DAGA CIKIN HARAMTACCE ILIMIN TAURARI AKWAI:

- Koyon *burujai* da da'awar sanin sa'a da mahuda, da abin da zai faru a *burujai*, wannan munkari ne da ya yadu..
- Gaibu babu wanda ya sanshi sai Allah.
- Allah - SWT - Ya ce: ***﴾Ka ce wadanda suke sammai da kasa ba su san gaibu ba sai Allah﴿***[1].
- Allah - SWT - Ya ce: ***﴾[Shi ne] Masanin gaibu, sannan ba Ya tsinkayar da gaibun nasa ga wani. Sai manzon da Ya yarda da shi, shi kuma lallai ya kan sanya masa tsaro ta gabansa da bayansa﴿***[2] Ai lallai yana tsinkayar da manzanninSa a kan wani gaibun kamar yadda ya tsinkayar da manzonSa - SAW - a kan Alkur'ani da abin da yake cikinsa na gaibu, idan Ya yi nufin saukar masa da wahayi sai ya sanya masa mala'iku masu tsaro suna tsare shi daga shaidanu.
- Daga cikin ilimin taurari haramtacce akwai: Karanta tafin hannu da *finjani* da kuma yin zane a ciki yashi.
- Duk wannan yana daga cikin da'awar sanin gaibu, kuma mai yinsa yana ta'amuli ne tare da shaidanu.
- Haramun ne ga musulmi ya rika tambayarsu, kai! Ko zallar tafiya inda suke, ko da ba da niyyar gasgatawa ba.
- [Annabi] SAW ya fada cikin abin da Abdullahi bn Abbas - R.A - ya rawaito**: "Wanda ya ɗosani wani abu na ilimin taurari, to, ya ɗosani wani kaso na sihiri, in ya ƙara ya ƙaru"**[3].
- Tsakanin Iilimin sanin taurari da sihiri akwai dangantaka ta hanyar da'awar sanin gaibu, da ta'amuli da shaidanu a cikin kowanne.

***Darasi na ashirin da uku ya karte tare da godewa Allah***

****

---

1 - Surat al-Naml: Ayoyi na 26 -27.
2 - Surat al-Jinn: Ayoyi na 26-27.
3 -Abu Dawud ne ya rawaito shi da isnadi ingantacce.

## (24)

## [WARWARE SIHIRI]

**WARWARE SIHIRI:**

- Shi ne warware sihiri ga wanda aka yi wa sihirin.
- **KALA BIYU NE:**

1) Warwarewa da sihiri irinsa.
2) Warwarewa ta hanyar *Raƙya* da *Ta'awiza* irin ta shari'a.

- **NA FARKON** haramun ne; saboda yana daga cikin aikin Shaidan.
- An karbo daga Jabir cewa Manzon Allah - SAW - an tambayeshi game da warware sihiri, sai ya ce: **"Yana daga cikin aiki shaidanu"**[1].
- Abin nufi da wannan *Nushra* (warware sihiri) wadda ta zo a hadisi ita ce *Nushrar* da aka saba da ita 'yan *jahiliyya* suna yinta, to, ita ce aikin Shaidan.
- Ba mai iya warware sihiri sai mai yin sihiri, kuma zuwa wajen masu sihiri da tambayarsu haramun ne, Saboda fadinsa [Annabi] SAW: "Wanda ya je wa boka sai ya gasgata shi bisa abin da ya fada, to, hakika ya kafircewa abin da aka saukarwa [Annabi] Muhammad – SAW -".
- Saboda mai sihiri ba zai iya kai wa ga warware sihiri ba sai ta hanyar ta'ammuli tare da shidanu, wanda ya tanbaye shi warware sihiri, to, ya taimaka masa a kan kafirci.
- NA BIYU: Warware sihiri ta hanyar *Ruƙya* ta shari'a da sunayen Allah da kalamanSa da abin da aka samu daga Annabi - SAW - na bangaren *Ta'awizai* na shari'a.
- Wannan nau'in ya halatta, hakika an tambayi Manzon Allah - SAW - game da *Ruƙya*? sai ya ce: **"Ku bijiro min da *Ruƙyarku*, babu laifi game da *Ruƙya* matukar ba ta zamo shirka ba"**

**YANA DAGA NAU'IN *RUƘYA* DA TAKE LALATA SIHIRI DA IZININ ALLAH AKWAI:**

1) Karanta Surat Al-Bakarah, hakika [Annabi] SAW ya ce: **"Lallai riko da ita albarka ne, barinta asara ne, zauna-gari-banza ba za su iya ba"** ai masu sihiri (matsafa).

---

1 -Ahmad ne ya rawaito shi da sanadi mai kyau.

2) Daga ciki akwai karanta Ayatul-Kursiyyi da ayoyi biyunkarshe na Surat Al-Bakarah.
3) Daga ciki akwai yin *Rukya* da ayoyin sihiri na *Ta'awizai*.

Hakika [Mala'ika] Jibrilu ya yi wa Annabi – SAW - *Rukya* da *Ta'awizai* a lokacin da aka yi masa sihiri – SAW -.

4) Daga cikin abin da zai taimaka wajen haka shi ne yin bincike game da sihirin da kuma lalata shi.
5) Daga cikin abin da zai taimaka wajen gano sihirin ko kuma wanda ya yi masa sihirin akwai rokon Allah – SWT -, Hakika Annabi - SAW - ya yi addu'a ne har Allah Ya sanar da shi [inda] sihirin ya ke, kamar yadda [Nana] A'isha - R.A - ta ce: **"Har zuwa wani lokaci da rana ko da dare alhalin yana wajena, sai ya yi addu'a, ya kuma yin adddu'a, sannan ya ce: "Ya A'isha ko kin san Allah Ya ba ni amsa cikin abin da na tambayeshi"**.

### 🕮 DAGA CIKIN ABIN DA ALLAH YA KE TSARE MUMINI DA SHI DAGA TSAFI AKWAI:

1) Karanta Al-Kur'ani musamman Surat al-Bakarah.
2) Kulawa da Azkaar na safiya da maraice.
3) Yin sammakon cin dabino guda bakwai, idan ya kasance na *Ajwar* Madina ne; to, ya fi falala.
4) Fadar: *La'ilaha illal lahu wahdahu la sharika lahu, lahul mulku wa lahul hamdu wa huwa ala kulli shai'in kadir* sau dari a safiya, da irinta a maraice.

### 🕮 ALALMOMIN MAI SIHIRI (MATSAFI)

Domin ka gane bambanci tsakanin mai sihiri (matsafi) da kuma wanda ya ke yin *Rukya* ta shari'ah, to, shi mai sihiri yana da wasu alamomi da za a ganeshi da su, daga ciki akwai:

- Za ka ganshi fasiƙi a yanayinsa da ɗabi'unsa.
- Za ka ganshi ƙazami a fuskarsa da tufafinsa da gidansa.
- Zai nemi wani abu na wanda aka yi wa sihirin kamar tufafinsa na ciki ko rawaninsa ko tagiyarsa da sauransu.

- Zai umarci mara lafiyar da ya yi yankan dabba ko tsuntsu da yake da wasu siffofi ayyanannu kamar ya kasance baƙi ƙirin a baƙin, ko wani waje ayyanane bayan faduwar rana , wanda shi ne lokacin bazuwar shaidanu, kuma kada a yi Bismillah a lokacin yankan.
- Daga cikin alamominsa zai rika yin wani gurnanin da mara lafiyar ba zai fahimta ba a lokacin yin tawaida, wanda hakan neman agajin shaidanu ne, kuma zai iya rubuta masa tawaidar da wasu saƙandamai da wasu abubuwa da ba a fahimta, kuma zai iya rubuta wani abu na Al-Kur'ani domin bagarar da mutane.
- Lallai mumini ya kiyayi masu sihiri (matsafa), da kuma fakewa da su. Kawai ya yi kankan da kai zuwa ga Allah - SWT - wajen neman lafiya.

**DON KARIN FA'IDA:**

- Ka duba littafin: Zad al-Ma'ad Na Ibn al-Kayyim , Fasalin Tsarin (Annabi) SAW Wajen maganin sihiri.
- Da littafin: Al-Sarim al-Battar, Na Sheikh Abdus- Salam Bali.

***Darasi na ashirin da hudu ya kare tare da godewa Allah.***

****

## (25)

## [KWAIKWAYON KAFIRAI , DA HUKUNCINSA DA NAU'O'INSA)

### KWAIKWAYO DA MA'ANARSA:

- Shi ne mai kwaikwayo ya aikata abin da ya kebanci wanda ya ke kwaikwaya ta bangaren Akida ko ayyuka ko shiga (sutura) da sauransu.
- Allah - SWT - Ya ce: ***[Yahudawa da Nasara ba za su taba yarda da kai ba har sai ka bi addininsu. Ka ce: "Shiriyar Allah lallai ita ce shiriya". Idan har ka bi son zuciyarsu bayan abin da ya zo maka na gaskiya, to, ba ka da wani majibinci ko mai taimakonka a wajen Allah)*** [1] .
- Ibn Kathir - R.A - Ya ce: A cikinsa akwai tsawatarwa da narko ga al'umma game da bin hanyoyin Yahudawa ds Nasara bayan abin da suka sani na Al-Kur'ani da Sunna, Allah Ya tsare mu daga haka.
- Allah - SWT - Ya ce: ***[Kuma kada ku kasance kamar wadanda suka rarrabu , kuma suka sassaɓa bayan hujjoji sun zo musu, wadannan kuwa suna da azaba mai girma)*** [2] .
- Abin nufi da su su ne Yahudawa da Nasara, an hana mu kasancewa irinsu.
- Daga Abdullahi dan Amr - R.A - ya ce: Manzon Allah – SAW - ya ce wanda ya kwaikwayi wasu mutane ya zama dan cikinsu"[3].
- Sheikhul Islam Ibn Taimiyah - R.A - Ya ce: Wannan hadisin mafi karancin yanayinsa (ma'anarsa) shi ne cewa yana hukuntar da cewa haramun ne yin kamanceceniya da su.
- Daga Amr bn Shu'aib daga babansa daga kakansa lallai Manzon Allah - SAW - ya ce: **"Wanda ya yi kamanceceniya da wanimmu, to, ba ya cikimmu, kada ku yi kamanceceniya da Yahudawa ko Nasara, hakika sallamar Yahudawa ita ce yin nuni da yatsu, ita kuma sallamar Nasara ita ce nuni da tafin [hannu]**"[4].
- Dalilai game da haka suna da yawa , har ma Ibn al-Kayyim - R.A - Ya ce: Akwai hadisai sama da dari a kan wannan asali.

---

1 - Surat al-Bakarah: Aya ta 120.
2 - Surat alIImaran: Aya ta 105.
3 -Abu Dawud ne ya rawaito shi.
4 - Tirmiziy ne ya rawaito shi.

### 🕮 ƘA'IDA GAME DA KWAIKWAYO:

- Sheikh Ibn al-Othaimin R.A ya ce: Abin auna kawaikwayon shi ne mai kwaikwayo ya yi abin da ya kebanta ne da wanda ya kwaikwaya, kwaikwayon kafirai shi ne musulmi ya aikata wani abu daga kebance-kebancensu, amma abin da ya yadu a tsakanin musulmai har ya zama ba a bambance kafirai da shi, to, baya zama kwaikwayon [da ake magana akai]. Maganarsa ta kare.

### 🕮 HALAYEN KWAIKWAYON KAFIRAI:

- **NA FARKO:** A cikin al'amuran addini kamar Akidu da Ibadu, daga ciki akwai bukukuwa wannan an hana shi sake-ba-kaidi.
- **NA BIYU:** Kamanceceniya da su a al'amura na al'ada kamar shiga (kayan sawa) da tufafi da sauransu, in ya kasance daga irin abin da suka kebanta da shi ne kuma musulmai ba sa yinsa, to, kwaikwayonsu haramun ne, idan kuma ba su kebanta da shi ba, to, ba ya cikin kwaikwayo haramtacce.
- **NA UKU:** Cikin al'amura na duniya kamar tsarin mulki , da tsarin sojoji, da tsare-tsaren da ba sa cin karo tare da Shari'ar Musulunci, wannan ba ya cikin abin da aka hana.

### 🕮 YANA DAGA CIKIN BARNACE-BARNACEN KWAIKWAYON KAFIRAI:

- Lallai kwaikwayonsu a zahiri yana gadar da kwaikwayonsu a baɗini a cikin aƙida da ɗabi'u.
- Huzaifa - R.A - ya ce: shiga (ta tufafi) ba ta yin kama da shiga har sai ɗabi'a ta yi kama da ɗabi'a.
- Lallai kwaikwayonsu yana tasowa ne daga raunin da mutum ya ke da shi. Da karayar zuciya, da kuma ganin banƙayen abin da suke a kai.
- Saboda wannan ne Allah Ya nuna mana yin kwaikwayo da Manzanni - A.S - saboda abin da Allah Ya ba su na siffofin da suka sanya suka cancanci a yi koyi da su.
- Ibn Khaldun ya ce: Saboda haka ne za ka ga a kodayaushe wanda aka yi galaba a kansa ya ke kwaikwayon wanda ya yi galabar a tufafinsa da abin hawansa da makaminsa ...
- Lallai kwaikwayon kafirai mataki ne na yin watsi da tsarin Musulunci da narkewa a duniya, muna rokon Allah yafiya.

- Lallai kwaikwayonsu a cikin abubuwan addininsu ana daukarsa a matsayin yarda da addininsu na barna.

***Darasi na ashirin na biyar ya kare tare da godewa Allah.***

****

**(26)**

## [ZIYARAR KABURBURA, HUKUNCINTA DA NAU'O'INTA)

- [Annabi] SAW ya ce: **"Na kasance na hanaku ziyarar kaburbura, to, [yanzu] ku ziyarce su, lallai tana tunatarwa a kan lahira"**

**ZIYARAR KABURBURA KALA UKU CE:**

- **NA FARKO:** Ziyarar da shari'a ta yarda da ita domin tuna lahira da yin addu'a ga matattu.
- Mustahabbi ne idan ya ziyarci makabarta ya ce: Assalamu alaikum gidan mutane muminai , mu ma in sha Allahu nuna nan za mu riskeku, Allah Ya gafarta mana da su, sai ya yi musu addu'a.
- **NA BIYU:** Ziyara ta shirka domin rokon matattu da neman agajinsu da neman madadi daga ruhinsu, ko kuma yi musu yanka da yi musu bakance ko Dawafi a kan kaburburansu, wannan nau'in babbar shirka ne, muna rokon Allah Ya amintar da mu.
- **NA UKU:** Ziyarar kaburbura domin karatu a wajensu ko yin sallah a wajensu ko yin yanka don Allah a wajensu, ko don karanta fatiha a ruhin mamaci, wannan bidi'a ce haramtacciya tana daga cikin hanyoyin shirka.
- Daga cikin abin da za riskar da wannan nau'in shi ne niƙar gari domin ziyarar kaburbura wannan abu ne da aka hana, ma'anar niƙar gari shi ne yin balaguro da nufin ziyarar wani kabari ayyananne, duk daya ne ko kabarin Annabi - SAW - ko waninsa daga Ahlul Baiti da waliyyai da salihai.
- Saboda fadar Annabi - SAW - : **"Kada ku niƙi gari sai dai zuwa masallatai uku, Masallacin harami da masallaci mafi nisa (Ƙudus) da wannan masallacin nawa".**
- Idan ya yi nufin ziyarar masallacin annabi - SAW - to, sai ya zama yana biye ne da ziyarar masallacin Annabi, kada ya yi balaguro da nufin ziyarar kabarin Annabi - SAW -, sai dai ziyararsa ta kasance ta biyo bayan ziyarar masallacin Annabi – SAW-.
- Idan ya yi sallah a masallacin sai ya tafi domin ya yi sallama ga Annabi - SAW - da sahabbansa biyu.
- Ba a son ayi ta maimaita ziyarar kabarin Annabi - SAW -, saboda fadarsa - SAW -: **"Kada ku dauki kabarina a matsayin idi (biki), ko [kusanya]**

**gidajenku su zama makabarta, ku yi min salati, lallai salatinku yana isa gareni a duk inda ku ke".**

- Ma'anar hadisin shi ne ba ya lazimta ace duk lokacin da mutum ya yi nufin yin salati ga Annabi - SAW - sai ya tafi wajen kabarinsa domin ya yi masa salatin daga kusa, hakika sallar bawa tana isa ga Annabi - SAW - a duk inda mai yi masa salatin ya ke.
- Domin samun karin bayani a kan wannan maudu'i sai a duba littafin: Ziyarar kaburbura da neman agajin na kabari, Wallafar Sheikhul Islam Ibn Taimiyah - R.A -.

***Darasi na ashirin da shida ya kare tare da godewa Allah.***

****

**(27)**

## [[ANNABI] MUHAMMAD - SAW - CIKAMAKIN ANNABAWA)

### 🕮 KA SANI YA KAI ƊAN UWANA MUSULMI:

- Lallai yana daga cikin imani da manzancin [Annabi] Muhammad - SAW - : Yin Imani cewa shi ne cikamakin Annabawa babu wani annabi bayansa.
- Allah - SWT - Ya ce: ***[ [Annabi] Muhammad bai kasance uban daya daga cikin mazajenku ba, sai dai [ shi ] ya kasance Manzon Allah ne, kuma cikamakin Annabawa ]***[1].
- Annabi - SAW - ya ce: **" ..Ni ne Akibu {wanda na biyo bayan Annabawa] a bayan sa babu kowa".**[2]
- [Annabi] SAW ya ce: **"Lallai za a samu wasu makaryata talatin a cikin al'umata kowannensu yana raya cewa shi annabi ne, ni ne cikamakin Annabwa, babu Annabi bayana"**[3].
- [Annabi] SAW ya ce: **"An fifita ni a kan sauran annbawa da abubuwa shida: … an rufe annabawa da ni"**[4].
- Wadannan dalilai da sauransu suna nuni a kan cewa shi [Annabi] SAW shi ne cikamakin Annabawa, kuma cewa babu wani annabi bayansa.
- Duk wanda ya kudurce cewa za a aiko wani annabi bayan [Annabi] Muhammad – SAW-, to, shi kafiri ne imaninsa bai inganta ba.
- Duk wanda ya yi da'awar annabta bayan [Annabi] Muhammad, to, shi kafiri ne, kamar Musailima al-Kazzab da al-Aswad al-Ansiy da Mirza Gulam al-Kadiyaniy wadanda suka yi da'awar annabta.
- Ƙungiyar Ƙadiyaniyya da suka bi shi Ƙungiya ce kafira, ta fita daga musulunci da musumai, kamar yadda malamai suka yi *Ijma'i* a kan haka a wannan zamanin.

---

1 - Sarat al-Ahzab: Aya ta 40.
2 - Bukhari da Muslim ne suka rawaito.
3 - Tirmiziy da Abu Dawud suka fitar da shi, asalinsa yana cikin Sahihu Muslim.
4 - Muslim ne ya rawaito shi.

- Ya zo a cikin hadisin da ya gabata **“Lallai za a samu makaryata talatin a cikin al’ummata … Hadith”.**
- Abin nufi –Allah ne Masani- wadanda suke da karfi da sojoji, in ba haka ba ai wadanda suka yi da’awar annabta sun fi haka.

***Darasi na ashirin da bakwai ya kare tare da godewa Allah.***

****

## (28)

## [WAJIBCIN IMANI DA ƘADDARA ALHERINTA DA SHARRINTA)

### ƘADDARA:

- Ita ce ƙaddarawar Allah **ga** kasantattu gwargwadon abin da ya zartar da shi a iliminSa da hikimarSa.

### ITA ƊIN MATAKIN HUƊU CE:

- **NA FARKO:** Ilimi, sai mu yi imani cewa Allah - SWT - Masani ne da komai, Ya san abin da ya kasance da abin da zai kasance, da abin da bai kasance ba wanda da ya kasance yaya zai kasance.
- **NA BIYU:** RUBUTU: sai mu yi imani cewa Allah - SWT - Ya rubuta duk abin da zai kasance a har zuwa tashin alkiyama.
- Allah - SWT - Ya ce: ***[Shin ba ka sani ba cewa Allah Ya san abin da yake cikin sammai da kasa, lallai hakn yana cikin Littafi, lallai hakan mai sauki ne a wajen Allah]***[1].
- **NA UKU:** GANIN DAMA: Sai mu yi imani cewa Allah - SWT - Ya so duk abin da ya ke sammai da kasa, babu wani abu da ya ke kasancewa face da ganin damarSa, duk abin da Allah Ya so sai ya kasance, abin da bai so ba ba zai kasance ba.
- **NA HUDU:** HALITTA, sai mu yi imani cewa Allah - SWT - [ Shi ne Mahaliccin komai, Shi ne Majibincin komai ][2].
- Wadannan matakai sun kunshi abin da zai kasance daga Allah - SWT - daga bayi.

***Darasi na ashirin da takwas ya kare tare da godewa Allah.***

****

1 - Surat al-Hajj: Aya ta 70.
2 - Surat al-Zumar: Aya ta 62.

## (29)

## [WAJIBCIN IMANI DA KADDARA ALHERINTA DA SHARRINTA KASHI NA (2))

- Sai kuma mu yi imani da cewa duk abin da bayi suke yi na maganganu da ayyuka ko bari sanannu ne a wajen Allah , a rubuce suke a wajenSa , kuma Allah Ya ga damarsu ne ya halicce su ne.
- Allah - SWT - Ya ce: ***[Wanda ya ga dama a cikinku sai ya daidaita, ba za ku ga dama ba sai in Allah Ya so Ubangijin talikai].***[1]
- Allah - SWT - Ya ce: ***[ Da Allah Ya ga dama da ba su yi fadan ba, sai dai Allah Yana aikata abin da ya yi nufi]***[2].
- Allah - SWT - Ya ce: ***[Allah ne Ya halicceku da abin da ku ke aikatawa)***[3].
- Tare da haka mun yi imani cewa Allah Ya sanyawa bawa iko da zabi da su ne aikinsa ya ke kasancewa.
- Allah - SWT - Ya ce; ***[Ku je wa gonakinku ta yadda ku ka so]***[4].
- Allah - SWT - Ya ce: ***[Da sun yi nufin fita da sun yi mata tanadi]***[5].
- Allah - SWT - Ya ce: ***[Wanda ya so daga cikinku ya yi gaba, ko ya jinkirta]***[6].
- Allah - SWT - Ya fuskantar da umarni da hani zuwa ga bawa, wannan yana nuni a kan cewa yana da iko da zabi da ganin dama.
- Ubangijimmu Ya yi yabo ga mai kyautatawa bisa kyautatawarsa, ya zargi mai munanawa bisa munanawarsa, da ba don cewar aikin yana faruwa da nufin bawa ba da zabinsa –ba tilas ba- da yabon mai kyautatawa da ukuba ga mai munanawa ya zama zalunci, Allah - SWT - ya ya tsarkaka daga wasa da zalunci.
- Babu cin karo bisa godiyar Allah tsakanin abin da Allah Ya kaddara shi Ya halicce shi, da kuma aikin bawa da ganin damarsa.

---

1 - Surat al-Takwir: aya ta 28 – 29.
2 - Surat al-Bakara Aya ta 253.
3 - Surat al-Saffat: Aya ta 96.
4 - Surat al-Bakarah: Aya ta 223.
5 -Surat al-Taubah: Aya ta 46.
6 - Surat al-Mudathir: Aya ta 37.

***Akwai sauran darasin, Allah ne abin dogaro.***

***Darasi na ashirin da tara ya kare tare da godewa Allah.***

****

**(30)**

## [WAJIBCIN IMANI DA KADDARA ALHERINTA DA SHARRINTA KASHI NA (3))

- **Domin kammala abin da muka ambata a darasin baya..**

📖 **SAI MU CE:**

- Kaddara sirrin Allah ce cikin halittarSa, bai tsinkayar da wani mala'ika makusanci ba ko Annabi abin aikowa..
- Shari'a sananniya ce ga kowa, sassauka ce a cikin Al-Kur'ani da sunnah.
- Saboda wannan ba ya halatta mai saɓo ya kafa hujja da hukunci da kaddara a bisa kafircinsa da saɓonsa.
- Saboda mai saɓo yana wuce gaba ya yi saɓo bisa zaɓinsa ba tare da ya san Allah Ya kaddara masa shi ba.
- Domin babu wanda ya san kaddarar Allah - SWT - sai bayan afkuwar abin da aka kaddara ***[Babu wani rai da ya san abin da zai aikata gobe]***[1].
- Wanda ya kafa hujja da kaddara bisa kafirci ko aikin saɓo, za a ce da shi: Kai dai ka san cewa Allah Ya haramta kafirci da saɓo da abin da ka sani a cikin Al-Kur'ani da Sunnah , sai dai kai ba ka da sanin cewa saɓon an kaddara maka shi kafin ka aikata shi, me ya sa ba ka yi aikin da'a ba , ka kafa hujja da kaddara?
- [Wannan] yana daga cikin abin da ya ke nuna cewa mai kafa hujja da kaddara yana bin son ransa ne.

📖 **MUNA CEWA MAI AIKATA SAƁO MAI KAFA HUJJA DA KADDARA BISA SAƁONSA:**

- Da wani mutum zai dake ka  ya kwace maka dukiyarka ya tafi, shin za ka kyale shi ka ce wannan kaddarata ce? Shin za ka karbi hujjarsa da zai ce maka: Na doke ka ne kuma na karbi dukiyarka ne bisa kaddarar Allah? Ko kuwa za ka yi fushi ne ka dauki matakin daukar fansa a kansa da dawo da dukiyarka? Ba shakka mutum zai yi kokari iya yinsa domin daukar fansa a kan wanda ya yi masa ta'addanci, ba zai karbi hujjar cewa wannan mai ta'addancin kaddara ba ce.

1 Surat Lukman: Aya ta 34.

- To saboda me mai aikata sabo zai kafa hujja da kaddara a wajen sabon Allah ba zai yi kokarin magance cutar da take cikin zuciyarsa ba!?
- Za mu cewa mai sabo mai kafa hujja da kaddara a kan sabonsa: Da za ka yi niyyar balaguro zuwa wani gari kuma yana da hanya biyu, sai mutum mai gaskiya ya ba ka labarin cewa daya daga cikin [hanyoyin] a kwai abubuwan tsoro da wahalhalu, ta biyun kuma tana da aminci da sauki, lallai ta biyun za ka bi , ba zai yiwu ka bi ta farkon ba, ka ce lallai an kaddara maka ne ba, da kuma za ka yi hakan da mutane sun dauke ka a matsayin mahaukaci.
- Kafa hujja da kaddara a kan shirka – gujewa nauyin da ya hau kan mutum ne, kuma watsi ne da da'awar manzanni- ita ce hanyar mushrikai , Allah ya fada game da su [ Wadanda suke yin shirka za su ce: "Da Allah Ya ga dama , da ba mu yi shirka ba. Haka iyayemmu ma da ba su yi ba, kuma da ba mu haramta wani abu ba" kamar haka ne wadanda suka gabace su suka karyata [manzanni], har sai da suka dandani azabarmu. Ka ce : " Shin kuna da wata hujja ce da za ku fito mana da ita? Ba fa abin da ku ke bi sai zato, kuma ku [ba a kan komai kuke ba] face shaci-fadi"}[1].
- Sai Allah Ya ba da labari cewa ba su da hujja wajen kafa hujjarsu da hukunci da kaddara a kan shirkar da suke yi, kuma yadda lamarin ya ke ba su da komai sai shaci fadi da zato.

***Darasi na talatin ya kare tare da godewa Allah.***

****

1 -Surat al-An'am: aya ta 148.

Da wannan darasi ne wannan [karatun] mai dogon zango ya kare , tare da fatan za mu fara wani [karatun] mai dogon zango in sha Allah, Allah ne Abin dogaro.

****

**RUBUTAWAR**

Abdullahi Bn Sulaiman

A birni Riyadh

A 14/4/1441A.H

Tashar Abdullahi bn Sulaiman al-Muhana (telegram)

https://t.me/AbdullahAlmuhana